# FAYYATACCEN BAYANI
# A KAN
# SIFFAR SALLAR ANNABI (S.A.W)
# DA KURAKURAN MASALLATA

**أوضح البيان على صفة صلاة النبي صلى الله عليه وسلم** وأخطاء المصلين

NA

DR. ABUBAKAR MUHAMMAD ISA

Haƙƙin Mallaka (HM):
Cibiyar Fassara ta Ar-Rahyan

Adireshi:
Dr. Abubakar Fari Residence,
Juma Road, Mariri,
Maiduguri Road, Kano.
Nigeria.

GSM: 08036223067
Whatsapp: 07049325138
Email: *abuamatullahi83@gmail.com*

Tunatarwa:
Ba a yarda a buga ko a kwafi wani ɓangare na wannan littafi don yin amfani da shi ta kowace irin hanya ba, ba tare da izini daga Marubuci ko Cibiyar Fassara ta Ar-Rayhan ba.

An Fara Bugawa a Shekarar:
1445 = 2025

ISBN: 978-978-773-674-9

MAƊABBA'A:
Iconic Computer and Printing Services.
08033676155.

# بسم الله الرحمن الرحيم

# المقدمة

وصلي الله علي النبي الكريم المبعوث رحمة للعالمين وعلى صحابته أجمعين.

## GABATARWAR MAWALLAFIN LITTAFI

Da sunan Allah Mai rahama Mai jin ƙai, tsira da amincin Allah su ƙara tabbata ga fiyayyen halitta Annabi Muhammadu da iyalan gidansa, da sahabbansa bakiɗaya.

Wannan taƙaitaccen littafi ne da zai tattauna a kan wasu kurakurai da suka yawaita a cikin Sallah, wasu daga ciki bisa kuskure wasu kuma jahilci, da kuma fito da haƙiƙanin yadda Manzon Allah tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi yake Sallah, tun daga kabbarar harama zuwa sallama.

Da kuma bayyana irin hatsarin saɓa wa siffar Sallar Annnabi (S.A.W).

Haka zai fito da dalilai ingattattu daga taskar Sunnar Ma'aiki tsira da amincin Allah su ƙara tabbata a gare shi.

Haƙika na lura malamai da masu wa'azi da karantarwa suna bakin ƙoƙarinsu wajen fito wa da al'ummar musulmai yadda haƙƙoƙin Allah suke a kansu, da kuma haƙƙoƙin Allah; amma na lura wannan muhimmiyar ibada ta Sallah tana da matuƙar buƙatuwa zuwa ga tsettsefe haƙiƙaninta; saboda yawaitar yaɗuwar kurakurai, har ta kai ga sun zamo jiki ba a jin wani abu yayin aiwatar da su.

Wannan littafi shimfiɗaɗɗiyar hanya ce ta kawo ƙarshen waɗannan kurakurai ina fatan Al'ummar musulmai musamman ɗaliban illimi da malamai su rungume shi, wajen karanta shi, da fahimtar sa da kyau, sannan a aiwatar da abubuwan da ya ƙunsa a aikace.

Ina fatan mai karanta wannan littafi ya fahimce ni da kyau, ba shi da alaƙa da wata ƙungiya! Kaɗai ya dubi abin da haƙiƙanin Musulunci ya koyar a kanta; saboda haka dukkanin musulmi yana da alaƙa ta kai tsaye da wannan littafi.

A ƙarshe duk abin da ya zamo na daidai ne, dacewa ce da falala ta Allah, abubuwan da suke na kurakurai gazawata ce, ina fatan Allah ya yi min Rahama kuma ya karɓi waɗanda suka zama na daidai, ya kuma amfanar da al'ummar musulman duniya bakiɗaya. *Amin.*

# GODIYA

Da farko ina miƙa cikacciyar godiya ta ga Allah Maɗaukakin sarki mafi cancantar a godewa, wanda a cikin ni'imominsa ne ya sauƙaƙe wannan muhimmin aiki, sa'an nan godiya ga iyaye guda biyu. Waɗanda aikinsu ne da tarbiyarsu ya sanya aka hau hanyar koyo-da-koyarwa Allah ya saka musu da alheri, da kuma dukkanin malamaina tun daga makarantar allo; Firamare; Sakandare; makarantar gaba da sakandare jami'o'i da majalisai na ilimi, Allah ya saka musu gabaɗaya da mafi alherin sakamako.

Haka kuma dole in kaɗaita godiya ga bawan Allan da ya taimaka da tunaninsa, da dukiyarsa, da lokacinsa, Allah ya albarka ce shi, da zuriyyarsa.

Ba zan manta da kwamitin rubuta wannan littafi ba; Nafiu Sabiu Ahmad Mariri, da malam Ahmad Baba Yakasai, da irin jajircewarsu da tsayuwarsu wajen tsara wannan littafi da inganta shi.

Haka kuma, ina miƙa godiyata ga malaman da suka duba wannan littafi kuma suka rubuta gabatarwa a kansa (تقريظ), Farfesa Sani Musa Ayagi, da Dr Abubakar Umar Isa, da Dr Jibril Ɗalha. Haka kuma, ina miƙa saƙon godiya ga Dr. Nura Baba Yakasai, babban mallami a Kwaleji Ilimi ta Sa'adatu Rimi, Kano Saboda muhimmiyar gudunmawar da ya bayar wajen duba wannan littafi da kuma yin gyararraki. Sa'an nan babban aminina Sheikh Sukairaj Hafiz Imam, saboda gudummawarsa a kodayaushe a kan abin da ya shafi na'ura mai ƙwaƙwalwa da shawarwari kyawawa.

Haka kuma kwamitin (من أخلاق السلف), na malam Salisu da Ahmad da Aminu.

Dole in gabatar da keɓantacciyar godiya ga malamina Malam Sunusi Adam babban limamin masallacin Jibwis Mariri Kano, godiyar ba za ta gama cika ba sai ta gode wa malamina Farfesa Yahaya Mujahid babban malami a jami'ar Amadu Bello da ke Zariya (ABU), kuma babban limamin *Masallaciun Juma'a na Borno Road.*

Haka kuma kwamitin ƙirƙira na "Subulus-salam", da dukkanin wani wanda ya ba da gudummawa ta kowacce irin fuska Allah ya saka wa kowa da mafi alherin sakamako. Amin.

KUNSHIYA


Gabatarwar Mawallafin Littafi
Godiya
Kunshiya
Gabatarwa (Taƙriz) Ta Farko
Gabatarwa (Taƙrizi) Ta Biyu
Gabatarwa (Taƙriz) Ta Uku

1.0 FASALI NA FARKO
1.1 Ma'anar Sallah a Shari'a
1.2 Rukunan Sallah
1.3 Sunnonin Sallah
1.4 Mustahabban Sallah
1.5 Sharuɗan Sallah

2.0 FASALI NA BIYU
2.1 Lokutan Sallah
2.2 Hukuncin Sallah Kafin Lokacinta
2.3 Bigiren Da Ya Halatta Musulmi Ya Yi Sallah Da Wajen Da Ba Ya Halatta
2.4 Abubuwan Da Suke Ɓata Sallah
2.5 Sujjadar Rafkanwa
2.6 Falalar Sallah

3.0 FASALI NA UKU
3.1 Kurakuran Niyyar Sallah
3.2 Kurakuran Karatun Sallah
3.3 Kurakuran Tsayuwa Da Ruku'u Da Sujjada
3.4 Kurakuran Ruku'u
3.5 Kurakuran Sujjada
3.6 Kurakuran Sallama Da Bayan Sallama
3.7 Wasu Daga Kurakuran Masallata Game Da Sallah

4.0 FASALI NA HUƊU
4.1 Maganganun Malamai a Game Da Sallah a Gaban Liman

4.2 Haƙiƙanin Siffar Sallar Annabi
4.3 Bayanin Malamai a Kan Sallar Annabi
4.4 Tasirin Yin Irin Sallar Annabi
4.5 Hatsarin Saɓa Wa Sallar Annabi


KAMMALAWA
JERIN LITATTAFAN DA AKA DUBA

GABATARWA TA FARKO

TAKRIZ

# بسم الله الرحمن الرحيم، وصلى الله على النبي الكريم

Bayan haka, na duba littafin da ɗan'uwa Dr Abubakar Muhammad Isa ya wallafa mai taken: "Fayyataccen Bayani a kan siffar sallar Annabi (صلى الله عليه وسلم), da kurakuran da masallata ke aiwatarwa". Kuma na ga littafin ya taɓo batutuwa masu muhimmanci da suka shafi Sallah tun daga ma'anarta, da shika-shikanta, da bayanin kurakuran da suke afkuwa yau-da-gobe, daga masallata, sannan ya yi bayani game da siffar Sallar Manzon Allah (صلى الله عليه وسلم), babu shakka gwani ya yi ƙoƙari wajen futo da muhimman abubuwa, ina ba da shawarar a mallaki wannan muhimmin littafi, kuma a karanta shi, a yi aiki da shi.



Prof. Sani Musa Ayagi
(Bayero **University** Kano)
Limamin Masallacin Juma'a na Jami'ar Bayero, Kano (BUK).

GABATARWA TA BIYU

DA SUNAN ALLAH MAI RAHAMA MAI JINKAI

*Taƙrizi*

Lallai wannan Littafin yana da Muhimmanci sosai ga dukkanin Musulmi, saboda fayyatattunn bayanai da ke ciki a Hausance game da Sallah, wadda ita ce ginshiƙin addini kuma farkon abin da za a yi wa bawa hisabi Ranar Tashin Kiyama. Littafin ya ƙunshi bayanai a kan ma`anar Sallah, farillanta, sunnoni, Mustahabbai, abubuwan da ke ɓata Sallah, ƙabali da ba`adi da sauran Hukunce Hukuncen Sallah, kuma Mawallafin Dr. Abubakar Muhammad Isa, ya yi matuƙar ƙoƙari wajen fayyace Abubuwan da littafin ya ƙunsa waɗanda Sallah ba ta ingantuwa sai da su, saboda haka ne ma nake kira ga al'ummar Musulmi bakiɗaya da su rungumi wannan Littafin don sauke mafi girman Ibadun kamar yadda aka wajabta.

Dr. Abubakar Umar Isa,
Department of Islamic Studies,
**University** of Maiduguri (UNIMAID).

# GABATARWA TA UKU
# TAKRIZ

بسم الله والصلاة والسلام على رسول الله
الحمد القائل: (اتْلُ مَا أُوحِيَ إِلَيْكَ مِنَ الْكِتَابِ وَأَقِمِ الصَّلَاةَ إِنَّ الصَّلَاةَ تَنْهَى عَنِ الْفَحْشَاءِ وَالْمُنْكَرِ وَلَذِكْرُ اللَّهِ أَكْبَرُ وَاللَّهُ يَعْلَمُ مَا تَصْنَعُونَ )[1] والقائل (إِنَّ الصَّلَاةَ كَانَتْ عَلَى الْمُؤْمِنِينَ كِتَاباً مَوْقُوتاً)[2] أقرأ الصلاة والسلام على رسول الله القائل: "صلوا كما رأيتموني أصلي" والقائل: " واعلموا أن من أفضل الأعمال الصلاة".

Bayan haka na samu damar karanta wannan littafi mai suna "Fayyataccen Bayani a kan Siffar Sallar Manzon Allah tsira da amincin Allah su ƙara tabbata a gare shi", na samu gamsuwa da jin daɗi matuƙa, bisa dalilai kamar haka:

1. Ganin yadda mawallafin littafin ya taƙaita bayanai, ta yadda mai karatu zai karance littafin cikin sauƙi, ba tare da ya gundira da karatun ba.
2. Littafin ya ƙunshi duk wasu muhimman bayanai da mai salla yake buƙatar sani, domin sallarsa ta inganta.
3. Duk muhimman bayanan da ke cikin littafin sun samu madogara daga ingantattun Hadisai, da kuma bayanan malamai magabata na ƙwarai.
4. Abu na ƙarshe kuma mafi muhimmanci shi ne; buga wannan littafi da harshen Hausa, lallai hakan zai ba wa al'umma da yawa dama waɗanda ba sa jin Larabci; don su fahimci yadda za su yi wannan mafificiyar ibada ta sallah, kamar yadda Annabi ya koyar.

Ina mai roƙon Allah Subhanahu Wata'ala da ya sanya wa wannan littafi albarka, ya sanya dubannin mutane su amfana da shi.
Shi kuma Gwani Abubukar Muhammad Isa muna roƙon Allah Subhanahu Wata'ala da ya ƙara masa hazaƙa da hikima da basira a kan wannan namijin ƙoƙari da ya sa a gaba, na wallafa da kuma fassara muhimman litattafan addinin Musulunci zuwa harshen Hausa.

Dr. Jibril Ɗalhat
Hukumar kula da harshen Larabci da addinin Musulunci ta ƙasa (NBAIS).
20/04/2024.

---

[1] Suratul Ankabut aya ta (45)
[2] Suratun Nisa'I aya ta (103).

# GABATARWAR ƊAB'I

Da Sunan Allah Mai Yawan Rahama Mai Yawan Jinƙai.
Tsira da Aminchin Allah su tabbata ga Annabi Muhammad (S.A.W).

A ƙoƙarin ɗabba'a wannan littafi na samu damar nazartarsa tare da fahimtar saƙonni guda biyu da littafin ke ɗauke da su ga ɗokacin al'ummar musulmi, musamman ma matasa.

Saƙo na farko, wanda shi ne maƙasudin littafin, shi ne ingantuwar sallahr duk wanda ya karanta littafin da nutsuwa da kuma lura. Ingantar sallah kuwa ba komai take nufi ba face kyautata ibada wadda ka iya zama sular samun yardar Ubangiji. Saƙo na biyu kuma, shi ne salon yadda marubucin ya rubuta littafin na iya taimakawa wajen ƙara dasa ɗabi'ar karatu ga musamman matasa wanda hakan ba ya nufin komai face tallafar yunƙurin samun al'umma makaranciya. Kacokam, littafin na nufin taimakawa wajen samar da nagartacciyar al'umma wadda ta samu yardar ubangiji.

Don haka nake yabawa da yunƙurin marubucin, Dr. Abubabar Muhammad Isa, tare da yi masa fatan samun ƙwarin gwiwar cigaba da wannan aiki na alheri da ya saka a gaba. Makaranta kuma, nake masu fatan samun natsuwa don karanta littafin don samun rabauta daga tarin amfanun saƙonnin dake ƙunshe cikin wannan littafi mai albarka.

Bissalam,

Muhd Nuraddeen Ado Gezawa.
Maɗabba'ar Iconic Computer and Printing Services.
No. 7., Juma Street,
Mariri Along Maiduguri Road, Kano.

# 1.0 FASALI NA FARKO

Wannnan fasali zai yi Magana ne game da sallah a dunƙulenta, da abubuwan da ta ƙunsa, kamar:

1.1 Ma'anar Sallah a Shari'a
1.2 Rukunan Sallah
1.3 Sunnonin Sallah
1.4 Mustahabban Sallah
1.5 Sharuɗan Sallah

Malaman musulunci sun yi bayani a kan ma'anar Sallah a harshe da ma'anarta a shari'ar musulunci.

- Abin da ake nufi da Sallah a harshe ita ce: Addu'a

Ubangiji Maɗaukaki yake cewa Annabinsa tsira da amincin Allah Su ƙara tabbata a gare shi:

(خُذْ مِنْ أَمْوالِهِمْ صَدَقَةً تُطَهِّرُهُمْ وَتُزَكِّيهِمْ بها وَصَلِّ عَلَيْهِمْ إِنَّ صَلاتَكَ سَكَنٌ لَهُمْ وَاللَّهُ سَمِيعٌ عَلِيمٌ)

*"Ka karɓi sadaka daga dukiyoyinsu, kana mai tsarkake su, kuma kana mai tabbatar da kirkinsu da ita. Lallai addu'o'inka nutsuwa ce gare su. Kuma Allah mai ji ne masani".*

A Wannan aya ma'anar Sallah tana nufin addu'a.

A wata surar kuma Allah Maɗaukaki ya ce:

(أُولئِكَ عَلَيْهِمْ صَلَواتٌ مِنْ رَبِّهِمْ وَرَحْمَةٌ وَأُولئِكَ هُمُ الْمُهْتَدُونَ)

*"Waɗannan da akwai albarku a kansu daga Ubangijinsu da wata Rahama. Kuma waɗannan su ne shiryayyu".*

A wannan aya kuma kalmar Sallah tana nufin yabo da albarka.

(وَما كانَ صَلاتُهُمْ عِنْدَ الْبَيْتِ إِلاَّ مُكاءً وَتَصْدِيَةً )

*" Kuma Sallarsu a wurin Ɗakin ba ta kasance ba face shewa da tafi".*

A wannan aya ma'anar Sallah tana nufin irin ibadar da musulmai suke ta bautawa Ubangiji da ƙanƙan da kai zuwa gare shi.

A wata ayar cikin Suratut Tauba Ubangiji Mabuwayi ya ce:

(وَمِنَ الأَعْرابِ مَنْ يُؤْمِنُ باللهِ وَالْيَوْمِ الآخِرِ وَيَتَّخِذُ مَا يُنْفِقُ قُرُباتٍ عِنْدَ اللهِ وَصَلَواتِ الرَّسُولِ)

*"Kuma daga cikin ƙauyawa akwai waɗanda suke yin imani da Allah da ranar Lahira, kuma suna riƙon abin da suke ciyarwa (tamkar) waɗansu ibadodin neman kusanta ne a wurin Allah da addu'oi'in Manzonsa".*

Sallah a wannan aya tana nufin addu'ar Annabi, da neman ya nema musu gafara.
A cikin suratul Ahzab kuma Allah yake cewa:

(إنَّ اللهَ وَمَلاَئِكَته يصلونَ على النَّبي يَا أيهَا الَّذين آمنُوا صلوا عَلَيْهِ وسلموا تَسْلِيمًا)

*"Lallai Allah da Mala'ikunsa suna salati ga Annabi. Ya ku waɗanda suka yi imani! Ku yi salati a gare shi, kuma ku yi Sallama domin amintarwa a gare shi".*
Ma'anar Sallah a nan tana nufin yabo da girmamawa.
Allah Maɗaukaki yake cewa:

(وَلَوْلا دَفْعُ اللهِ النَّاسَ بَعْضَهُمْ ببَعْضٍ لَهُدِّمَتْ صَوَامِعُ وَبيَعٌ وَصَلَوَاتٌ وَمَسَاجِدُ يُذْكَرُ فِيهَا اسْمُ اللهِ كَثِيرًا).

*"Kuma ba domin tunkuɗewar Allah ga mutane ba, sashensu da sashe, haƙiƙa da an rusa Sauma'o'in (Ruhbanawa), da majami'o'in Nasara, da gidajen bautar Yahudu, da masallatai waɗanda ake ambatar Allah a cikinsu da yawa".*
A wannan aya Sallah tana nufin wajen bautar Yahudawa, watau inda suke gudanar da ibadunsu na Yahudanci.
Ubangiji Maɗaukaki da buwaya yake cewa:

(وَأَقِيمُوا الصَّلاةَ وَآتُوا الزَّكَاةَ وَأَطِيعُوا الرَّسُولَ لَعَلَّكُمْ تُرْحَمُون )

*"Kuma ku tsayar da Sallah, kuma ku bayar da zakka, kuma ku yi ɗa'a ga Manzo domin a yi muku Rahama".*
Ita ma wannan aya tana nufin ma'anar Sallah ta ibada, wacce aka wajabtawa Musulmai.

Waɗannan su ne waɗansu daga cikin ayoyin da suka yi magana a kan Sallah, tare da cewa kusan kowacce da akwai ma'anar da take ƙunshe da ita.

## 1.1 Ma'anar Sallah A Shari'a

Ma'anar Sallah a shari'a: Wata dunƙulalliyar ibada ce da take ƙunshe da addu'o'i, ƙasƙantar da kai, ayyuka, ruku'u da sujjada,wadda ake buɗeta da kabbara, ake kammalata da Sallama  da sharuɗa. A cikin wannan bayani na ma'anar Sallah a shari'ance; abin da ake nufi da addu'o' su ne waɗanda ake yi a ciki tun daga wacce ake yi ta farko (addu'ar buɗe Sallah) yayin  kabbarar harama kafin fara karatun Fatiha, har zuwa zikirin da ake yi lokacin ruku'u da ɗagowa, zuwa lokacin da mutum zai yi sujjada da abin da ake karantawa yayin zaman tahiya, zuwa Sallama da zikirin da suke biyo bayan Sallama.
Abin da ake nufi da aiki kuwa shi ne motsin mutum a cikin Sallar, tun daga tsayuwa da abin da ta ƙunsa, ruku'u da ɗagowa da zama a cikin Sallah, waɗannan su ne ayyukan mai Sallah.

## 1.2 Rukunan Sallah

Sallah tana da farillai da rukunai, waɗanda ingancinta yake ginuwa, har idan aka yi sakacin wani abu daga farillanta; saboda rashin sani, ko ganganci ko rafkanuwa take ɓaci, waɗannan rukunai guda goma sha huɗu ne:

- Tsayuwa lokacin Sallar farilla (idan da iko, lafiya).
- Kabbarar harama, saboda faɗin Manzon Allah tsira da amincin Allah su ƙara tabbata a gare shi: "Idan ka ta shi yin Sallah, to ka yi kabbara"
- Karatun Fatiha: Wajibi ne karanta Fatiha a kowacce raka'a; saboda faɗin Annabi tsira da aminci su tabbata a gare shi: "Babu Sallah ga wanda bai karanta Fatiha ba". Amma karatun Fatiha ban da wanda yake bin liman, shi ba wajibi ba ce a kansa a yayin da liman yake bayyanawa; sai dai malamai sun ce: Da zai karanata a tsattsakin (shirun liman a tsakanin ayoyin da yake karantawa na Fatiha) karatun liman da hakan ya fi kyau.

- Ruku'u da Nutsuwa a cikinsa: Watau ana so mutum idan zai yi ruku'u ya daidaitu kuma ya nutsu, saboda faɗin Ma'aiki tsira da amincin Allah su ƙara tabbata a gare shi: " Sannan sai ka yi ruku'i har sai ka nutsu kana mai ruku'i"
- Ɗagowa daga ruku'u da daidaituwa a tsaye.
- Yin sujjada a bisa gaɓɓai guda bakwai (goshi tare da hanci, tafukan hannaye biyu, gwiwowi biyu, da duga-dugai biyu) tare da nutsuwa.
- Ɗagowa daga sujjada
- Zama tsakanin sujjada guda biyu.
- Nutsuwa a dukkanin rukunan (Sallah).
- Tahiyar ƙarshe.
- Zama domin tahiyar ƙarshe.
- Yin salati ga Annabi tsira da amincin Allah su ƙara tabbata a gare shi; saboda bayanin da malamai suka yi a ƙarƙashin faɗin Abdullahi ɗan Mas'ud Allah ya ƙara masa yarda:" Mun kasance muna cewa aminci ya tabbata ga Allah daga bayinsa, sai Manzon Allah tsira da amincin Allah su ƙara tabbata a gare shi ya ce: Ka da ku ce aminci ga Allah daga bayinsa, kaɗai abin da za ku ce " Attahiyatu Lillahi….". Da wannan ne malamai suka ce ya nuna Tahiya wajibi ce.
- Jerantawa tsakanin rukunai.
- Sallama (watau faɗin masallaci a ƙarshen Sallarsa *Assalamu alaikum*).

### 1.3 Sunnonin Sallah

Sallah tana da sunnoni waɗanda idan an aikata su za a samu lada, rashin aikata su ba ya ɓata Sallah.

Sunnonin Sallah sun kasu gida biyu; Sunna *mu'akkada* (sunna mai ƙarfi) da Sunna *gairu mu'akkada* (wacce take zamantowa kamar mustahabi). Waɗannan sunnoni gabaɗaya su ne:

- Karatun sura, ko kuma wani abu na daga Alƙur'ani, kamar aya ɗaya ko biyu bayan karatun Fatiha, a Sallahr asuba da raka'o'in farko na Sallahr Azahar da La'asar, da Magriba, da Isha'i.

- Ɗaga hannuwa daidai kafaɗa, ko saitin kunne.
- Kallon wajen da za a yi sujjada a yayin Sallah.
- Addu'ar buɗe Sallah.
- Faɗin Amin (آمين) bayan kammala karatun Fatiha, kamar yadda hadisi ya zo a cikin Bukhari da Muslim, daga Annabi tsira da amincin Allah su ƙara tabbata a gare shi ya ce, "Idan liman ya ce Amin, to kuma ku faɗa; domin duk wanda (Amin) ɗinsa ta dace da ta Mala'ika, (to) an gafarta masa abin da ya gabata na laifukansa."
- Bayyana karatu a Sallar da ake bayyanawa, da ɓoyewa a Sallar da ake ɓoyewa.
- Yin shiru na ɗan'lokaci bayan gama karatu gabaɗaya.
- Miƙar da gadon baya ta yadda da za a ɗora ƙwarya ɗauke da ruwa a gadon bayansa ba za ta tuntsire ba, kamar yadda mata suke ɗigirgire da tulu.
- Riƙe gwiwoyi yayin ruku'i tare da yalwata (buɗe) yatsun hannu.
- Bayar da tazara tsakanin hannuwa yayin ruku'u.
- Gabatar da hannuwa a kafin gwiwoyi yayin yunƙurin tafiya sujjada.
- Haɗe 'yan yatsun hannu yayin sujjada.
- Fuskantar da yatsun hannu da na ƙafafuwa zuwa ga kallon alƙibla yayin sujjada. (Gabas ga mutanen dake ƙasashen dake yammacin Ka'aba).
- Bayar da tazara tsakanin gaɓoɓi a cikin sujjada.
- Sanya hannuwa kusa da kafaɗu, ko kusa da kunnuwa a yayin sujjada.
- Haɗe ƙafafu da dugadugai, da kafe su a yayin sujjada.
- Shimfiɗa ƙafar hagu da kafe ta dama a zama tsakanin sujjada biyu, da kuma zaman tashiyar farko.
- Ɗora hannun dama a kan cinyar dama, da na hagu a kan ta hagu, ko kuma ɗora tafukan hannu a kan gwiwa tsakanin sujjadu biyu.
- Dogaro da hannyaensa yayin tashi daga sujjada.

- Tashi daga sujjadar ta biyu zuwa wata raka'ar; yana mai dogaro da hannunsa.
- Ya zamanto zamansa a cikin tahiya irin wanda aka ambata ne (na siffar Sallar Annabi) (S.A.W).
- Addu'a da neman tsari daga abubuwa guda huɗu, (azabar kabari; azabar jahannama; fitinar rayuwa da mutuwa), bayan tahiya ta ƙarshe, kafin Sallama.
- Sallama ta biyu (*Assalamu alaikum wa Rahmatullah, Assalamu alaikum wa Rahmatullah*).
- Ambaton Allah da Addu'a bayan Sallah (Ga ɗaiɗaiku).

Wato zikiran da aka rawaito Annabi tsira da amincin Allah su ƙara tabbata a gare shi, yana yin su, kamar faɗin *Astagfirullah* sau uku, *Allahuma Antas-salamu Wa minkas-salamu Tabarkta Ya- zaljalali Wal'ikram*, da kuma faɗin *Subhanallahi* talatin da uku; *Alhamdulillahi* talatin da uku; *Allahu Akbar* talatin da uku, da cikewa da faɗin "*Lailaha Illal-lahu Wahdahu La-sharika Lahu, Lahul Mulk, Walahul Hamdu, Wa huwa Ala kulli Shai'in Kadir*" sau ɗaya.

### 1.4 Mustahabban Sallah

Sallah ibada ce mafi girma a cikin ibadu, don haka ta ƙunshi farillai da sunnoni, da mustahabai.

Mustahabbi; wani abu ne da ake son maSallahci ya zo da shi a cikin Sallah; shi ya sa malamai suka saki alƙalami wajen bayyana su; duk da barinsu ba ya ɓata Sallah; sai dai samun ragi na yawan lada.

Mustahabban Sallah su ne kamar haka:

- Ɗaga hannaye biyu yayin kabbarar harama kusa da kunnuwan masallaci ko kafaɗunsa.
- Yin karatun Sallah ga mamu yayin da liman yake karatu a sirrance.
- Faɗar *Amin* bayan karatun Fatiha.
- Jeranta surorin karatu (watau idan aka karanta sura a raka'a ta farko, to, a raka'a ta biyu za a karanta wacce take ƙasanta, kamar; *Kulhuwallahu*, *Falaƙi*, *Nas*.... ).

- Yin karatu tare da tsawaita shi: Akwai sallolin da ake so a tsawaita karatunsu; kamar Sallar Asuba, da Sallar Azahar.
- Taƙaita karatu: A Sallar La'asar da Magriba, da yin tsaka-tsaki a Sallar Isha'i.
- Ambaton Allah a lokacin ruku'u ( سبحان ربي العظيم ). Da sauran zikirorin da suka zo yayin ruku'u.
- Faɗin (رَبَّنا وَلك الحمد), yayin da liman ya ce (سَمِعَ الله لِمن حَمِده).
- Ɗora hannaye akan gwiwoyi yayin ruku'u.
- Gabatar da hannuwa kafin gwiwowi, yayin da mutum zai yi sujjada.
- Daidaita hannuwa kusa da kunnuwa yayin sujjada.
- Addu'a a yayin sujjada.
- Gajarta zaman tahiyar farko a kan na biyu.
- Addu'a bayan kammala tahiyya ta biyu, da cike ta da Istigfari kafin Sallama.
- Karkaɗa ɗan yatsan nuni yayin tahiya ko miƙar da shi, da dunƙule ragowar yan'yatsu huɗun, da kallon gefen ɗanyatsan har a yi sallama.
- Ɗora hannun hagu a kan cinya.
- Damantawa da fuska yayin Sallama (wato karkata kunci ɓangaren dama).

## 1.5 Sharuɗan Sallah

Sharuɗan ingancin Sallah suna cika daga waɗannan abubuwa masu zuwa:

- SANIN SHIGAR LOKACI: Saboda faɗin Allah Maɗaukaki:

**(إِنَّ الصَّلَاةَ كَانَتْ عَلَى الْمُؤْمِنِينَ كِتَاباً مَوْقُوتاً)**

"Lallai ne Sallah ta kasanc a kan muminai, farilla mai ƙayyadaddun lokuta".

Don haka, Sallah ba ta inganta kafin shigar lokacinta ko bayan fitarsa, sai da wani karɓaɓɓen uzuri a shari'ar Musulunci. (Kamar mantuwa ko halin tafiya).

- TSARKAKA DAGA KARI GUDA BIYU: (fitsari da bayan gida), saboda faɗinsa Maɗaukaki:

(يا أَيُّهَا الَّذِينَ آمَنُوا إِذا قُمْتُمْ إِلَى الصَّلاةِ فَاغْسِلُوا وُجُوهَكُمْ وَأَيْدِيَكُمْ إِلَى الْمَرَافِقِ وَامْسَحُوا بِرُؤُسِكُمْ وَأَرْجُلَكُمْ إِلَى الْكَعْبَيْنِ وَإِنْ كُنْتُمْ جُنُباً فَاطَّهَّرُوا)

*"Ya ku waɗanda suka yi iman! Idan kun tashi zuwa ga Sallah, to, ku wanke fuskokinku da hannuwanku zuwa magincirori (gwiwar hannaye) , kuma ku yi shafa ga kanku, kuma ku (wanke) ƙafafunku zuwa idanun sawu biyu. Kuma idan kun kasance masu janaba, to, ku yi tsarki".*

Haka kuma Hadisi ya zo daga Abdullahi ɗan Umar, Allah ya ƙara masa yarda, daga Annabi tsira da amincin Allah su ƙara tabbata a gare shi ya ce: " Allah ba ya karɓar Sallah ba tare da tsarki ba".

- TSARKIN TUFAFI DA JIKI DA WAJEN DA ZA A YI SALLAR: Dalili a kan tsaftar tufafi faɗinsa Maɗaukakin Sarki:

(وَثِيَابَكَ فَطَهِّر)

*"Kuma tufafinka sai ka tsarkake su."*

Da kuma faɗin Manzon Allah tsira da amincin Allah su ƙara tabbata a gare shi: "Idan ɗayanku ya je masallaci, to, ya juya takalmansa ya gani; idan ya ga wata ƙazanta, to, ya goge ta a ƙasa, sannan ya yi Sallah da kayansa".

Shi kuwa tsarkin jiki faɗinsa tsira da amincin Allah su ƙara tabbata a gare shi ga Aliyu ɗan Abi Ɗalib, dangane da tambayar da ya aiki Miƙdad zuwa ga Annabi (Tsira da Amincin Allah su ƙara tabbata a gare shi) game da maziyyi, sai ya ce: "Ka yi alwala, sannan ka wanke al'aurarka". Sannan ya cewa mai al'ada "Ki wanke jikinki".

TSARKIN MUHALLI: Muhalli anan yana nufin bigiren da za a yi Sallah; a masallaci, kasuwa, ma'aikatun gwamnati ko kamfanoni da sauransu. Saboda faɗin Annabi tsira da amincin Allah su ƙara tabbbata a gare shi ga sahabansa, game da Baƙauyen da ya yi fisari a cikin masallaci: "Ku kwara ruwa a kan fitsarinsa".

Wanda yayi Sallah da akwai najasa a tare da shi, kuma bai san da ita ba, to, Sallarsa ta inganta kuma ba zai sake ba. Idan kuma ya ganta a

lokacin da yake Sallar idan zai iya kawar da ita, kamar ya zamanto tana takalminsa ko wanin ƙarin tufafin da ya ƙaru a kan wanda ya suturce al'aurarsa, to, ya kawar da ita, sannan ya cika Sallarsa. Idan kuma ba shi da ikon kawar da ita, to, ya yi sallarsa kuma ba zai sake ba.

- Suturce Al'Aura: Saboda faɗin Ubangiji Maɗaukakin Sarki:

  (يَا بَنِي آدَمَ خُذُوا زِينَتَكُمْ عِنْدَ كُلِّ مَسْجِدٍ)

  *"Ya ku 'ya'yan Adam! Ku riƙi adonku a wurin kowanne masallaci".*

  A da can larabawa sun kasance suna zagaye ɗakin Ka'aba babu tufafi.

  Da kuma faɗin Annabi tsira da amincin Allah su ƙara tabbata a gare shi: " Allah ba ya karɓar Sallar mai al'ada sai da mayafi".
- FUSKANTAR ALKIBILA: Saboda faɗin Ubangiji Maɗaukakin sarki:

(وَمِنْ حَيْثُ خَرَجْتَ فَوَلِّ وَجْهَكَ شَطْرَ الْمَسْجِدِ الْحَرامِ وَحَيْثُ مَا كُنْتُمْ فَوَلُّوا وُجُوهَكُمْ شَطْرَهُ)

*"Kuma daga inda ka fito, to, ka juyar da fuskarka a wajen masallaci Tsararre, kuma (Duk) inda kuke, to, ku juyar da fuskokinku a wajensa".*

Da kuma faɗinsa tsira da Amincin Allah su ƙara tabbata a gare shi, ga wanda ya munana Sallarsa: " Idan ka tashi yin Sallah, to, ka kyautata alwalarka, sannan ka fuskanci alƙibila".

Kuma ya halatta a kauce wa alƙibilar a yayin tsananin tsoro, da kuma Sallar nafila a halin tafiya a kan abin hawa.

Wanda ya kirdadi alƙibila, sai ya yi Sallah a ɓangaren da yake zaton nan ne alƙibila, sannan daga baya ya gane kuskurensa, to, ba zai sake Sallarsa ba. Kamar yadda Sahabi Amir ɗan Rabi'a, Allah ya ƙara masa yarda ya faɗa, ya ce: "Mun kasance tare da Annabi tsira da amincin Allah su ƙara tabbata a gare shi a wata tafiya cikin wani

dare mai duhu. Ba mu san a ina alƙibila take ba, sai kowanne mutum ya yi Sallarsa inda yake tsammani. Yayin da muka wayi gari sai muka ambaci haka ga Manzon Allah tsira da amincin Allah su ƙara tabbata a gare shi, sai wannan aya ta sauka:

**(وَلِلَّهِ الْمَشْرِقُ وَالْمَغْرِبُ فَأَيْنَمَا تُوَلُّوا فَثَمَّ وَجْهُ اللَّهِ إِنَّ اللَّهَ وَاسِعٌ عَلِيمٌ)**

*"Kuma Allah ɗai yake da gabas da yamma, saboda haka, inda duk aka juyar da ku, to, a can fuskar Allah take.. Lallai ne Allah Mawadaci ne mai Ilimi".*

- Niyya: Shi ne mutum ya yi niyyar Sallar da zai yi, sannan ya ayyana ta a zuciyarsa, babu buƙatar bayyana ta a zahiri.

## 2.0 FASALI NA BIYU

Wannnan fasali zai yi Magana ne game da lokutan sallah da wasu abubuwa da suka ƙunshi sallar:

2.1 Lokutan Sallah

2.2 Hukuncin Sallah Kafin Lokacinta

2.3 Bigiren Da Ya Halatta Musulmi Ya Yi Sallah Da Wajen Da Ba Ya Halatta

2.4 Abubuwan Da Suke Ɓata Sallah

2.5 Sujjadar Rafkanwa

2.6 Falalar Sallah

### 2.1 Lokutan Sallah

Sanin lokutan Sallah ga Musulmi abu ne mai muhimmanci, domin samun tabbaci da yaƙini wajen yin Sallarsa. Kuma addinin Musulunci ya wajabta wa Musulmai salloli guda biyar a kowacce rana, kuma cikin ƙayyadaddun lokutan da shari'a ta bayyana. Sanin lokutan Sallah da yin ta a lokutan da Allah ya umarta abu ne wanda ake so musulmai nagari su ɗore a kansa; domin hakan alama ce da take nuna imanin mutum, saboda faɗin Ubangiji Maɗaukaki:

(إِنَّ الصَّلاةَ كانَتْ عَلَى الْمُؤْمِنِينَ كِتاباً مَوْقُوتاً).

*"Lallai ne Sallah ta kasanc a kan muminai, farilla mai ƙayyadaddun lokuta".*

Annabi tsira da amincin Allah su ƙara tabbata a gare shi ya bayyana waɗannan lokuta daga bakinsa mai daraja da albarka, yake cewa: " Lokacin Sallar Azahar idan rana ta yi zawali (wato ta gota daga tsakiyar sama ta yadda inuwar mutum ta fara bayyana har zuwa daidai da tsawon mutum) matuƙar lokacin La'asar bai yi ba. Lokacin Sallar La'asar kuma; yana farawa daga daidaituwar inuwar mutum da tsawonsa, matuƙar rana bata yi fatsi-fatsi ba. Lokacin Sallar Magriba kuma yana farawa daga faɗuwar rana matuwar shafaƙi (jajatan bayan faɗuwar rana) bai ɓuya ba. Lokacin Sallar Isha kuma yana farawa ne daga gushewar shafaƙi (jajatan bayan faɗuwar rana)

zuwa rabin tsakiya na dare kafin fitowar alfijir. Lokacin Sallar Asuba kuma, daga ɓullowar Alfijir matuƙar rana ba ta ɓullo ba".

Cikin wannan hadisi na Manzon Allah tsira da Amincin Allah su ƙara tabbata a gare shi, ya bayyana mana lokutan kowacce Sallah a cikin waɗannan salloli na farilla guda biyar:

- Sallar Azahar: idan rana ta yi zawali (wato ta gota daga tsakiyar sama ta yadda inuwar mutum ta fara bayyana har I zuwa daidai da tsawon mutum) matuƙar lokacin La'asar bai yi ba.
- Sallar La'asar: Lokacin Sallar La'asar kuma; yana fara wa ne daga daidaituwar inuwar mutum da tsawonsa, matuƙar rana bata yi fatsi-fatsi ba.
- Sallar Magariba: Lokacin Sallar Magariba kuma yana farawa daga faɗuwar rana matuwar shafaƙi (jajatan bayan faɗuwar rana) bai ɓuya ba.
- Sallar Isha'i: Lokacin Sallar Isha kuma yana farawa ne daga gushewar shafaƙi (jajatan bayan faɗuwar rana) zuwa rabin tsakiya na dare kafin fitowar alfijir.
- Sallar Asuba: Lokacin Sallar Asuba kuma, daga ɓullowar Alfijir matuƙar rana ba ta ɓullo ba".

## 2.2 Hukuncin Sallah Kafin Lokacinta

An tambayi Sheikh Usaimin Allah ya yi masa Rahama game da yin Sallah kafin lokacinta, sai ya ce: "Sallah kafin lokacinta ba ta yiwu ba, ko da kuwa minti ɗaya ya rage kafin lokacinta to, Sallarsa ba ta inganta ba, saboda Allah ya ce " Lallai Sallah ta kasance ga muminai a ƙayyadajjen lokaci". Sallah ba ta inganta kafin lokacinta, kuma wajibi mutum ya sake waccan Sallahr da ya yi kafin lokacinta, Allah ya datar damu".

Haka kuma cewa: "Sallah kafin lokacinta ba ta inganta a bisa haɗuwar malamai (ijma'in mallamai). Idan mutum ya yi Sallah kafin lokacin, idan da ganganci ya yi, to, Sallarsa ta ɓaci, kuma bai kuɓuta daga laifi ba. Amma idan ba da gangan ya yi ba, saboda zatonsa ko lokacin ya shiga, to ba mai laifi ba ne, Sallarsa da ya yi

ta zama nafila; wajibi ne ya sake Sallar; saboda yana daga cikin sharuɗan ingancin Sallah shigar lokaci".

## 2.3 Bigiren Da Ya Halatta Musulmi Ya Yi Sallah Da Wajen Da Ba Ya Halatta

Hadisi daga Annabi tsira da amincin Allah su ƙara tabbata a gare shi ya ce: "Dukkanin ƙasa masallaci ce, ban da banɗaki da maƙabarta". Ya zo a cikin wasu hadisai, Manzon Allah tsira da amincin Allah su ƙara tabbata a gare shi ya bayyana guraren da ba a yin Sallah. Daga cikin guraren da hadisan suka bayyana ba a yin Sallah a cikinsu sun haɗa da:

- Maƙabarta
- Banɗaki
- Magurfanar Raƙuma (wajen da suke zama, ko kuma turkensu).
  Kamar yadda ya zo a wani hadisin da aka tambayi Manzon Allah tsira da amincin Allah su ƙara tabbata a gare shi game da yin Sallah a magurfanar raƙuma, sai ya ce: "Kar ku yi Sallah a magurfanar Raƙuma, domin su daga Shaiɗan suke".

## 2.4 Abubuwan Da Suke Ɓata Sallah

Sallah a shari'ar Musulunci ita ce mafi giman ibadu; manyan malamai sun yi bayani a kan abubuwan da dole sai da su take inganta, sannan sun bayyana abubwan da suke ɓata ta, duk sanda ɗaya daga cikin abubuwa masu zuwa suka faru ga masallaci, to, dole sai ya sake Sallah, ko kuma gyara ta ta hanyar yin sujjadar rafkanwa.

- Zance da ganganci ba tare da wani gyara ko maslaha ga abin da ya shafi Sallah ba.
  An karɓo hadisi daga Abdullahi ɗan Mas'ud Allah ya ƙara masa yarda ya ce: Da mun kasance muna yi wa Manzon Allah tsira da amincin Allah su ƙara tabbata a gare shi Sallama, alhali yana cikin Sallah, sai ya mayar mana da amsa; yayin da muka dawo daga wajen Najashi (sarkin Habasha), sai muka yi masa Sallama (amma) bai mayar mana ba. Sai ya ce: "Lallai a cikin Sallah da akwai aiki".

- Ci da sha da gangan, Imamus Sa'adi, Allah yayi masa rahama ya ce: Sallah tana ɓaci, saboda ci ko shan wani abu a cikinta; sai abin da yake ƙanƙani (saboda) rafkanwa ko rashin sani..
- Barin wani rukuni ko sharaɗi daga cikin sharuɗanta, da gangan ko rafkanuwa, ko kuma a halin rashin sani; sai dai a hali na kasawa (gajiyawa).
- Barin wani wajibi daga cikin wajibanta da ganganci.
- Yawan motsi a al'adar mutane (watau motsin da a al'adar mutane suke ɗaukarsa a matsayin motsi mai yawa).
- Kyaƙyata dariya, Ibnu Munzir ya ce: malamai sun haɗu a kan ɓacin Sallar wanda ya ƙyaƙyata dariya. Imamun Nawawi ya ce: Sallar tana ɓaci ne idan haruffa biyu (wato ƙwayoyin sautin furuci) suka bayyana a cikin dariya.
- Warwarewar tsarki; domin sharaɗi ne daga cikin sharuɗan ingancin Sallah.
- Kauce wa alƙibila (watau inda mai Sallah yake fuskanta lokacin da yake Sallah), domin fuskantar alƙibila sharaɗi ne na ingantuwar Sallah.
- Yayewar al'aura. (watau bayyanar abin dake tsakanin gwiwa da cibiyar ɗa namiji).
- Niyyar fita daga Sallah, (watau idan masallaci ya ƙudurci niyyar fita daga Sallah, Sallar sa ta ɓaci ba tare da saɓanin malamai a ciki ba).

## 2.5 Sujjadar Rafkanwa

Abin da ake nufi da sujjadar rafkanwa ita ce: sujjadar da masallaci zai ƙara bayan kammala Sallarsa, kafin sallama ko bayan sallama; sakamakon tauye wani wajibi ko ƙari.

Wasu daga cikin ma'abota ilimi sun tafi a kan cewa yin sujjadar rafkanwa mustahabi ce; sai dai abin da ya fi rinjaye wajibi ce, saboda umarnin Annabi tsira da amincin Allah su ƙara tabbata a gare shi, "Idan ɗayanku yana Sallah, sai Shaiɗan yakan zo masa, sai ya sa masa shakku a cikin Sallarsa, har ya manta raka'a nawa ya

Sallata, idan ɗayanku ya samu kansa a (cikin irin wannan halin), to yayi sujjadu guda biyu yana zaune".

Wannan sujjadar tana da halaye guda biyu; wacce ake yi bayan Sallama (watau idan mutum ya gama Sallarsa gabaɗaya), wannan ita ake kira da (Ba'adi). Da kuma sujjadar da ake yi kafin Sallama, wacce ake kira da; (Kabali), dukkaninsu suna da hukunce-hukunce da dalilan da ya sa ake yin su.

- Wanda ya yi rafkanwa a cikin Sallarsa wajen ƙara raka'a ɗaya, ko sujjada ɗaya da makamantansu, wajibi ne a gare shi ya yi sujjada guda biyu, bayan idar da sallarsa, sannan ya yi sallama.
- Wanda ya bar wata sunnar wajibi daga cikin sunnonin sallah da ganganci, to, zai yi sujjada kafin sallamarsa, kamar ya bar zaman tahiyar tsakiya, bai yi ta ba, ko kuma ya tuna bayan ya yunƙura a tsaye, to, ba zai dawo ba saboda haka; zai yi sujjada kafin sallama.
- Wanda ya yayi sallama a cikin sallarsa kafin ta gama cika, to zai sake, idan a kusa ne (watau bai ɗauki lokaci mai tsawo ba), to sai ya cika sallarsa, kuma ya yi sujjada guda biyu bayan sallama. Kamar yadda hadisi ya zo lokacin da Annabi tsira da amincin Allah su ƙara tabbata a gare shi ya yi sallama a raka'a ta biyu; sai Zul-yadain ya tambaya shin an rage adadin raka'o'in da ake yi ne, ko kuma ka manta ne? Sai Manzon Allah tsira da amincin Allah su ƙara tabata a gare shi ya cika sallar, sannan ya yi sujjada biyu bayan sallama.
- Wanda ya manta sujjadar Ba'adi zai yi ta a lokacin da ya tuna, ko da ya kasance sama da shekara ne.
- Ba a yin sujjadar rafkanwa ta Kabali, sai an bar sunnoni guda biyu ko sama da haka, amma barin sunna guda ɗaya; to babu sujjada a kanta, sai dai a wajen ɓoyewa da bayyanawa, wanda ya ɓoye a wajen da ake bayyanawa, zai yi sujjada kafin sallama; wanda kuma ya bayyana a wajen da ake ɓoyewa, to, zai yi sujjada bayan Sallama, haka shi ma wada yayi zance yana mai rafkanwa, to, zai yi sujjada bayan Sallama.

- Wanda ya manta yayi Sallama a raka'o'i biyu yana mai rafkanwa, to, zai yi sujjada bayan Sallama, haka shi ma wanda ya ƙara raka'a ɗaya ko biyu (a cikin Sallarsa) zai yi sujjada bayan Sallama.
- Wanda ya manta bai yi zaman farko ba, zai yi sujjadar rafkanwa; idan hanayensa ko gwiwoyinsa, sun rabu da ƙasa, lokacin da ya yunƙura zai tashi, idan kuma basu rabu (da ƙasa) ba, to, babu rafkanwa a kanshi.

Wanda ya tashi a raka'a ta biyu ya manta bai yi tahiya ba, to, zai yi sujjada kafin sallama, kamar yadda hadisi yazo daga Annabi tsira da amincin Allah su ƙara tabbata agare shi: "Idan ɗayanku yayi shakku a cikin sallarsa, bai san (raka'a) nawa ya Sallata ba; biyu ko huɗu, to ya kore wannan shakkun ya gina Sallarsa a kan abin da yake da yaƙini; sannan yayi sujjadu guda biyu, kafin yayi Sallama".

- Wanda yayi kokwanto game da wata raka'a ko sujjada, to, ba zai zo da ita raka'ar ba, sai yayi sujjada bayan Sallama (Ba'adi).
- Babu sujjadar (rafkanwa) ga wanda ya ƙara karatun sura a raka'o'in biyun-ƙarshe, da mutumin da ya ji an ambaci Annabi Muhammad tsira da mincin Allah su ƙara tabbata a gare shi, (sai yayi masa salati).
- Amma wanda yayi rafkanwa a bayan liman, to babu sujjada a kansa, a wajen mafi yawan malamai; amma (idan) limaminsa yayi rafkanwa, to zai yi sujjada tare da shi; saboda wajibcin yin koyi da liman.

## 2.6 Falalar Sallah

Sallah aba ce mai girma, kuma rukuni daga rukunan Musulunci, wanda yake wajibi ne cikaccen Musulmi ya gudanar da salloli guda biyar na farilla a kowanne dare da yini, haka wannan ibada tana daga cikin abubuwa mafiya girma da falala a Musulunci, daga cikin abubuwan da suke nuna falalar Sallar da girmanta suna da yawa, kamar yadda ayoyin Alƙur'ani da hadisan Annabi tsira da amincin Allah su ƙara tabbata a gare shi suka yi bayani, kamar:

- Faɗin Ubangiji Maɗaukaki inda yake bayyana halayen muminai:

- (الَّذِينَ يُؤْمِنُونَ بِالْغَيْبِ وَيُقِيمُونَ الصَّلاةَ وَمِمَّا رَزَقْناهُمْ يُنْفِقُونَ).

  *"Su ne waɗanda suka yi imani da gaibu, kuma suke tsayar da Sallah, suke ciyarwa daga abin da muka azirtasu".*

- و قوله : (وَأَقِيمُوا الصَّلاةَ وَآتُوا الزَّكاةَ وَارْكَعُوا مَعَ الرَّاكِعِينَ)

*Kuma da faɗinSa "Kuma ku tsayar da Sallah ku bayar da Zakka, ku yi Sallah tarer da masu Sallah".*

- و قوله (وَاسْتَعِينُوا بِالصَّبْرِ وَالصَّلاةِ وَإِنَّها لَكَبِيرَةٌ إِلاَّ عَلَى الْخاشِعِينَ)

  *Da faɗinsa "Ku nemi taimakon Allah ta hanyar yin haƙuri da tsaida Sallah, Lallai ita Sallah tana da girma; sai ga masu tsoron Allah".*

- (إِنَّما وَلِيُّكُمُ اللهُ وَرَسُولُهُ وَالَّذِينَ آمَنُوا الَّذِينَ يُقِيمُونَ الصَّلاةَ وَيُؤْتُونَ الزَّكاةَ وَهُمْ راكِعُونَ).

*"Kaɗai Majiɓincinku shi ne Allah da ManzonSa da waɗanda suka yi imani suke tsayar da Sallah suke bayar da Zakka, kuma suke Sallah tare da Masallata".*

Ubangiji Maɗaukaki ya bayyana siffofin muminai, da abubuwan da suke aikatawa; daga cikin waɗannan siffofi Sallah tana cikinsu, kamar yadda yake a cikin faɗinsa:

**(وَالْمُؤْمِنُونَ وَالْمُؤْمِنَتِ بَعْضُهُمْ أَوْلِيَآءُ بَعْضٍ يَأْمُرُونَ بِالْمَعْرُوفِ وَيَنْهَوْنَ عَنِ الْمُنْكَرِ وَيُقِيمُونَ الصَّلَوٰةَ وَيُؤْتُونَ الزَّكَوٰةَ وَيُطِيعُونَ اللهَ وَرَسُولَهُ).**

"*Kuma muminai maza, da mata; sashensu majiɓancin sashe ne, suna umarni da kyakkyawa, kuma suna hani da mummuna, kuma suna tsayar da Sallah da bayar da zakka, kuma suna ɗa'a ga Allah da Manzonsa*".

Waɗannan, wasu daga cikin ayoyin Alƙur'ani mai girma ke nan da suke nuna girmanta da falalarta ga Musulmai, daga cikin hadisan Annabi tsira da aminci su ƙara tabbata gare si kuwa su ne:

- Faɗin Annabi tsira daamincin Allah su ƙara tabbata a gare shi: "*Tsakanin mutum da kafirci (shi ne) barin Sallah*".

- "*Kan al'amari (jagora) shi ne Musulunci, tushensa kuma Sallah. Kololuwar tozansa kuma (shi ne) yin yaƙi a tafarkin Allah*".
- "*An umarce ni na yaƙi mutane; har sai sun shaida babu abin bautawa da gaskiya sai Allah, kuma Annabi Muhammadu Manzon Allah ne, su tsayar da Sallah, su bayar da zakka, idan suka aikata haka, to, jininsu da dukiyoyinsu sun kuɓuta daga gare ni; sai da haƙƙin Musulunci kuma hisabinsu (sakamakonsu) na wajen Allah*".
- Faɗin Annabi tsira da amincin Allah su ƙara tabbataa gare shi yayin da aka tambaye shi game da, wane aiki ne ya fi falala, sai ya ce: *Sallah a lokacinta.*
- Annabi tsira da amincin Allah su ƙara tabbata a gare shi ya ce: "*Babu wani Musulmi da zai riski Sallar farilla, sannan ya kyautata alwalarta, da kushi'inta (nutsuwa da jin tsoron Allah), da ruku'inta; face sai ta zamo masa kaffara (kankarar zunuban) abin da ya gabace ta na zunubai*".

## 3.0 Fasali Na Uku

Wannnan fasali zai yi Magana ne game da mafi yawan kurakuran da masallata suke yi a cikin Sallah kamar:

3.1 Kurakuran Niyyar Sallah
3.2 Kurakuran Karatun Sallah
3.3 Kurakuran Tsayuwa  Zuwa Sujjada
3.4 Kurakuran Ruku'u
3.5 Kurakuran Sujjada
3.6 Kurakuran Sallama Da Bayan Sallama
3.7 Wasu Daga Kurakuran Masallata Game Da Sallah

### 3.1 Kurakuran Niyyar Sallah

Ya kai ɗan'uwa mai albarka ka sani cewa, duk lokacin da ka karɓi wani gyara a cikin wannan addini na Musulunci, to, ka turmutsa hancin Shaiɗan kuma ka hau hanyar da Allah yake so bawansa ya kasance, Allaah ya datar da kai.

Yana daga cikin kurakuran da suka shahara (yaɗu) a wajen masallata da yawa (shi ne); furta niyya a yayin fara Sallah, sai ɗayansu (daga cikin masu yin Sallar) ya ce: Na yi niyyar yin Sallah kaza, a (mazaunin gida), wataƙila ma ya ambaci adadin raka'o'inta, wannan kuwa kuskure ne. Saboda niyya a Mazhabar Imamu Malik, da mafi rinjayen malamai (shi ne) a zuciya ake yin ta.

Babu buƙatar harshe (ya furta), duk da cewa, wasu malaman Mazhabar  Malikiya, sun tafi a kan halaccin bayyanawa ga mai yawan wasuwasi (kwokwanto); domin ya kawar da kwokwanton daga gare shi, wajen samun niyyar Sallah(wato shi a haƙƙinsa mustahabbi ne).

Bayyana niyya (yayin Sallah) kuskure ne, kuma bidi'a ce wacce ta yaɗu, daga bakunan masallata masu yawa; ba tare da bambancewa wajen bin hanyar Annabi tsira da aminci ba, da kuma bin shiriyarsa.

Ba ya wajaba bayyana niyya da motsa harshe a ɓoye, kuma ba a son yin hakan a bisa ittifaƙin malamai, a'a, abin sani ma shi ne, wanda ya aikata hakan ya yi bidi'a, wanda ya saɓa wa shari'a. Kuma ya cancanta a yi masa horo na shari'a, bayan an yi masa bayani kuma

ya doge a kan aikata hakan; musamman ma idan yana cutar da wanda yake Sallah tare da shi, haka da yawa daga cikin malaman Musulunci suka tafi a bisa wannan zance.

Ibnul Kayyum Allah ya yi masa rahma ya ce: "Annabi tsira da amincin Allah su ƙara tabbata a gare shi ya kasance, idan ya tashi zai yi Sallah sai ya ce: Allahu Akbar, ba ya faɗar wani abu kafinta, bai taɓa bayyana niyya kwata-kwata ba, kuma bai taɓa cewa zan yi Sallar kaza ba a (lokacin) da yake fuskantar alƙbila a (salloli masu) raka'a huɗu, (ko ƙasa da haka, shi ne) yake limancin ko bi yake yi, kuma bai taɓa cewa (Sallar) yanzu (nake ba) ko ramuwa.

Wannan ƙirkiraren abu ne  (mai girma), kwata-kwata babu wanda ya karɓo (wannan magana) da ingantaccen isnadin (hadisi) ko mai rauni, ko Musnadi, ko Mursali, (wanda yake bayyana) niyya kwata-kwata, kai, ko ɗaya daga cikin sahaban (Annabi; Tsira da Amincin Allah su ƙara tabbata a gare shi), haka kuma babu waɗanda suke ganin kyawun hakan daga cikin Tabi'ai, haka ma manyan malaman nan guda huɗu. Amma game da abin da wani sashe na Shafi'iyya suka tafi a kai na bayyana niyya, har suke kafa hujja wajen haka da maganar Imamush Shafi'I na cewa: "Babu wanda zai fara ta sai da Ambato", kuskurensu ne.

Imamun Nawawi ya ce: "Mutanenmu (malamanmu na Shafi'iyya), suka ce: Mai wannan maganar yayi kuskure, ba Shafi'i yana nufin furta (niyya) a cikin Sallah ba, a'a, abin da yake nufi (shi ne) yin kabbara".

Ibnul Kayyum ya ce: Abin da ya ruɗi wasu daga cikin na baya-baya, game da maganar Imamush-shafi'i (Allah  yayi masa rahama) shi ne faɗinsa game da Sallah, ita ba kamar azumi ba ce, babu wanda zai fara ta, face da ambatonta. Sai suka yi zaton cewa tunawar shi ne mai Sallah ya bayyana niyya. Abin sani, (shi ne) abin da Shafi'i yake nufi da tunawa (ambato) ita ce kabarar harama. Idan ba haka ba, ta yaya Shafi'I zai halatta abin da Annabi tsira da amincin Allah su ƙara tabbat a gare shi bai aikata a Sallarsa ko sau ɗaya ba;  ko ɗaya daga cikin Halifofinsa, da Sahabansa.

Ibnul Abil'iz ya ce: "Babu wani daga cikin malaman Mazhaba guda huɗu, ko Shafi'I da waninsa, (wajen) kafa sharaɗin bayyana niyya, abin sani ita niyya a zuci take, a bisa haɗuwarsu ( a kan niyya)". Akwai Nassoshin Shari'a tabatattu masu yawan da ba za su ƙidayu ba, da suke ƙarfafa; hadisin Aisha Allah ya ƙara mata yarda, inda take cewa, "*Annabi tsira da amincin Allah su ƙara tabbata a gare shi ya kasance yana buɗe sallarsa da kabbara*".

- Wasu daga cikin masallata suna fara Sallah, ta farilla ko (wasu) keɓantattun na nafilfili kamar, Sallar idi, da ta idin layya, da raka'o'i biyu na alfijir ba tare da iyakance ainihin Sallar da za su yi ba, wannan kuskure ne; wanda zai iya bayuwa ga ɓacin Sallar da rashin isarta .

Haka na daga cikin kurakuran da suka yaɗu:

Bayyana (niyyar) Sallah da keɓance ta (wace zai yi) a wajen da mutum zai yi Sallah, (duk da kasancewarta Azahar ko La'asar, ko ta rashin lafiyar wata, ko ta roƙon ruwa) wajibi ce a sallolin farilla, da na nafilla waɗanda suke da keɓantattun da wurin (da ake yi).

- Daga cikin mutane akwai masu ganin halaccin (niyya da kabbarar harama su zamo a tare), ko kuma wajabta hakan, wannan abu ne da hankali (zai yi aiki a wajen) saboda ita kabbara da kuma bayyana lafazinta, babu makawa tana cikin zuciya, to, ta yaya zai yiwu (a haɗa niyya da kabbara a haɗe a lokaci guda) alhali zuciya ta shagaltu da niyya? (Watau a hankalce ma hakan ba zai taɓa yiwuwa ba).
- Wasu daga cikin masu yin sallah sukan kudiri niyyar yin wata Sallar, sai su yi kuskure, sai su saki harshe, ko kuma su yi rafkanwar bayyana wacce take ba ita ba, ko kuma su yi suɓutar baki; sai su ƙudurce cewa hakan ya ɓata Sallahrsu, ƙudurce hakan na (ganin ɓacin Sallah, ga wanda yayi suɓutar baki wajen niyya) kuskure ne. Bai tabbata daga cikin litattafan mazhaba ba (cewa) idan lafazi ya saɓa wa niyya Sallah ta ɓaci ba; abin lura game da niyya (shi ne) idan haka ya faru ne (ga mutum) yana mai rafkanwa, ba da ganganci ba, misalin haka

kamar: Idan mutum a zuciyarsa yayi niyyar Sallar Azahar, sai kuma ya furta Sallar La'asar da bakinsa (yana) mai rafkanwa, to, Sallarsa ingantacciya ce.

- Daga cikin mutane akwai wanda zai haramar yin sallarsa shi kaɗai; sai (bayan ya tayar da Sallah) sai ya samu wasu mutane suna Sallah a kusa da shi; sai ya bi (watau sai ya jona Sallarsa da su) wannan Sallar da haramarsa ta farko; domin (ya samu Sallar) don fatansa riskar Sallahr jam'i, wanda haka kuskure ne, wanda yake ɓata Sallah a wajen malaman mazahaba.

Haɗɗab ya ce: Abin da yake daidai game da zantukan malaman mazhaba shi ne: Sharaɗi ne wajen cikar ingancin Sallah, mai bi ya yi koyi da liman (wajen niyyar harama) a farkon Sallah; idan ya yi niyyar koyi da shi a ya yin da ake Sallar, to, ta ɓaci.

Ya kai ɗan'uwa mai albarka ka sani cewa, duk lokacin da ka karɓi wani gyara a cikin wannan addini na Musulunci, to, ka turmutsa hancin Shaiɗan kuma ka hau hanyar da Allah yake so bawansa ya kasance, Allah ya datar da kai.

### 3.2 Kurakuran Karatun Sallah

- Yana daga cikin kurakuran da masallata suke yi rashin tsayawa a kan aya, (hakan ) ya yawaita a tsakanin limamai, na rashin tsayawa a kan aya, sai wasu daga cikinsu su dinga karanta Suratul Fatiha aya biyu-biyu, (suna haɗe wata da wata), ai har cikinsu ma ana samun wanda yake karanta ta gabaɗayanta ba tare da yayi numfashi ba, har zuwa ƙarshenta, (yin hakan) abu ne da ya saɓa wa tabbatacciyar Sunna daga Annabi tsira da amincin Allah su ƙara tabbata a gare shi.

An tambayi Ummu Salama Allah ya ƙara mata yarda game da karatun Annabi tsira da Amincin Allah su ƙara tabbata a gare shi, sai ta ce: "*Yana tsayawa a karatunsa a kan kowacce aya*".

Ibnul Kayyum ya ce: "*Ya kasance yana jan sautinsa, yana tsayawa a ƙarshen kowacce aya*". (Tare da kyutata karatun).

Imamud Dani ya ce: "*Jama'a daga cikin magabata, da makaranta Alƙur'ani na baya, sun kasance suna son tsayawa a kan ayoyi; ko*

*da sashensu ya kasance haɗe da juna.*" (Wato ayar farko tana da dangantaka da aya ta biyun).

- Kuskuren wajen karatun Fatiha abu ne da ya (yaɗu) a wajen gama-garin mutane da yawa, daga cikin wannan kuskuren da akwai wanda yake canza ma'anar, kai, yana kai wa ma ga ɓata Sallah, kamar wajen faɗin *an'amtu* maimakon *an'amta* ( صِرَاطَ الَّذِينَ **أنعمتُ**) haƙiƙa mutum ya sanya ni'imar a karan kansa (watau kamar shi mutum ɗin ne ya jingina ni'imar a kansa, saboda canza wasalin "Ta" I zuwa "Tu") ba ta ɓangaren Ubangiji Mabuwayi ba, (wanda yin hakan) kuskure ne da yake ɓata Sallah, (saboda haka) wajibi ne a gare shi ya zauna a wajen wanda zai gyara masa karatun Fatiha, da ayoyin da yake karanta wa daga littafin Allah.
- Daga cikin wani kuskuren da mutane suke yi, musaman yayin karatun Fatiha wajen karanta (الْحَمْدُ لِلَّهِ), ta yadda wasu suke canza asalin ma'anar *'Lillahi'* zuwa "*Dillahi*" watau (لِلَّهِ) da (دِللَّهِ), wanda shi ma yin haka ɓata ma'anar Alƙur'ani ne, haka da canza kowacce kalma daga asalinta izuwa wani abu daban.
- Yana daga wani kuskuren da ake yi yayin karatun Fatiha wajen canza wasalin (الرحْمنِ) "*Arrahmani*" sai ake kuskure wajen furtawa ana cewa (الرحْمنُ) "*Arrahmanu*" wanda furta hakan shi ma kuskure ne, yadda yake shi ne "*Arrahmani*" ba "*Arrahmanu*" ba.
- Yana daga cikin kurakuren dai da ake yi yayin karanta Fatiha akwai kuskuren biya (يَوْ) wajen (يَوْمِ الدين) sai ake kuskuren biyawa wajen da furto "*Yo*". Abin da yake daidai shi ne "*Yau*" ba "*Yo*" ba ne.
- Yana daga wani kuskuren da masallata suke, akwai rashin ƙarfafa harafin shadda a (إِيَّاكَ) "*Iyyaka*" sai a ake furta shi ba tare da shadda ba (إِيَاك) "*Iyaka*" wanda shi ma yin hakan kuskure ne; abin da ake so a furta idan an zo faɗa shi ne a ƙarfafa wasalin shadda da yake kan" '*Ya'un*", saboda haka abin da yake daidai shi ne: "*Iyyaka*" ba "*Iyaka*" ba.

Mawwaƙ ya ce: "Ibnul-ƙassar da Alƙadi Abdulwahab suka ce: Yin Sallah a bayan mai yawan ɓata ma'anonin Alƙur'ani, ba ta halatta idan wannan lahanin yana canza ma'anar; kamar yi wa harafin "*Kafun*" ɗin "*Iyyaka*" kasara (sanya mata wasali a ƙasa), ko kuma sanya wa "*An'amta*" rufu'a. Kuma ya halatta ayi Sallah a bayansa idan kuskuren da yake ba ya canza ma'ana, kamar yi wa harafin "*Dalun*" ɗin Alhamdulillah, kasara (wasali ƙasa), ko kuma yi wa "*Ha'un*"ɗin Allahu rufu'a".

- Yana daga cikin kurakuran da ake yi, yayin furta (نَعْبُدُ) "*Na'abudu*" sai ake kuskuren canza wasalin harafin 'Ba'un' daga wajen ake sanya masa, wasali a ƙasa ake furta *na'abidu* (نَعْبِدُ), wanda karanta hakan kuskure ne, abin da yake daidai shi ne *Na'abudu* (نَعْبُدُ).
- Yana daga cikin kurakuran da ake yi yayin karatun Fatiha wajen canza lafazin asali na *sirada* (الصِّراط) zuwa kuskure wajen furta shi da (الصُّراط) "*Surad*" wanda hakan shi ma kuskure ne, daidai ɗin shi ne: "Sirad". (الصِّراط), da kasara a ƙasan "*Sadun*" ɗin.
- Haka shi ma wajen *an'amta* ""أنعمتَ, kamar yadda ya gabata.
- Yana daga cikin kurakuran da ake yi yayin furta *gairi* (غيرِ), da kasara wanda shi ne daidai, saɓanin haka shi ne furta *gairu* (غيرُ), watau yi wa "*Ra'un*" ɗin damma.
- Yana daga cikin kuskuren da masallata suke yi wajen canza ma'anar asali ta *maghdubi* (مَغْضُوبِ), wanda shi ne daidai, tare da faɗin "*Magarubi*, ko *Maggadubi*, ko *Magalubi*" wanda shi ma hakan kuskure ne (duk waɗannan abubuwan da aka ambata na kurakurai, ana samun waraka ne daga gare su, kaɗai idan aka je gaban malami aka koya a wajensa, kamar yadda Ma'aiki tsira da amincin Allah su ƙara tabbata a gare shi ya koyi karatu a gurun Malamainsa Jibrilu Alaihis-salam. Allah Maɗaukakin Sarki ya ce:

(وَإِنَّكَ لَتُلَقَّى الْقُرْآنَ مِنْ لَدُنْ حَكِيمٍ عَلِيمٍ).

"*Kuma Lallai ne kai, haƙiƙa*, ana haɗa ka da Alƙur'ani daga gun mai hikima".

Bisa waɗannan nassoshi da suka gabata da bayanan malamai ya zama wajibi mu koyi yadda ake karanta Fatiha a gurin malamai.

Ya kai ɗan'uwa mai albarka ka sani cewa, duk lokacin da ka karɓi wani gyara a cikin wannan addini na Musulunci, to, ka turmutsa hancin Shaiɗan kuma ka hau hanyar da Allah yake so bawansa ya kasance, Allah ya datar da kai.

### 3.3 Kurakuran Tsayuwa Zuwa Sujjada

Wasu daga cikin masallata suna yin kurakurai tun daga kan tsayuwa da ruku'u da sujjada, ta yadda ba sa cikacciyar tsayuwa wacce take tattare da nutsuwa da rashin daidaituwa, wajen cikar sahun Sallah, ko kuma shigar da wani abu wanda yake ba daidai ba. Daga cikin kurakuran da ake yi yayin tsayuwar Sallah sun haɗa da:

- Kuskure wajen yadda ake ɗaga hannaye yayin kabbarar harama. "Daga cikin mutane akwai wanda ba ya ɗaga hannayensa, kwata-kwata, a kabbarar harama ce ko waninta (yin) hakan abu ne da ya saɓa wa aikin Annabi tsira da amincin Allah su ƙara tabbata a gare shi. Da akwai kuma wanda yake yin kuskuren yadda ake ɗaga hannun, idan ya ɗaga hannayensa ba ya kusantar da su zuwa kunnuwansa, ko kuma kafaɗunsa, ko dai ya ɗaga hannayensa yana mai dunƙule su, ko kuma ya buɗe hannayensa yana mai yalwata su (kamar wanda zai yi zagi ko korar kaji) yayin ɗaga hannun".

Abin da yake daidai shi ne mutum ya ɗaga su daf da kunnuwansa, ko kuma kafaɗunsa, ba tare da ya dunƙule su ko ya rarrabe su ba. Kamar yadda hakan shi ne irin yadda Annabi tsira da amincin Allah su ƙara tabbata a gare shi yake yi a cikin Sallarsa "Ba ya buɗa hannayensa (warware su) kuma ba ya dunƙule su".

- Sannan da yawa daga cikin masallata ba sa daidaita sahunsu a yayin Sallah, wanda aikata hakan kuskure ne; domin Manzon Allah tsira da amincin Allah su ƙara tabbata a gare shi yayi umarni da daidata sahu a cikin Sallah.

Sheikh Usman ɗan Fodiyo Allah ya yi masa Rahama yake cewa game da ƙin daidaita sahu: "(Yin hakan) *bidi'a ce abar ƙyama*".

- Daga cikin kurakuran da masallata suke yi yayin tsaiwar Sallah da akwai, ɗora hannu a ciki ko kuma cibiya. Babu wani ingantaccn hadisi daga Annabi tsira da amincin Allah su ƙara tabbata a gare shi, da yake nuna ana ɗora hannu a wani waje idan ba a saman ƙirji ba. Sheikh Albani ya ce, "Ɗora hannu a kan ƙirji shi ne ya tabbata a cikin hadisi (wajen koyi da Annabi), saɓanin haka kuwa, ko dai ya zamo abu ne mai rauni, ko kuma wanda ba shi da asali ma".

Ya kai ɗan'uwa mai albarka ka sani cewa, duk lokacin da ka karɓi wani gyara a cikin wannan addini na Musulunci, to, ka turmutsa hancin Shaiɗan kuma ka hau hanyar da Allah yake so bawansa ya kasance, Allah ya datar da mu a duka sauran gurare.

### 3.4 Kurakuran Ruku'u

Mafi yawa daga cikin masallata suna yin kurakurai game da abin da ya shafi ruku'u, ta hanyar gabatar da wani ɓangare ko tauye wa, ba sa yin sa a yadda sifarsa da kamalarsa take. Daga cikin mutane da akwai masu ɗora hannayaensu a kan ƙwaurinsu ko cinyarsu." Sai dai Annabi tsira da amincin Allah su ƙara tabbata a gare shi ya kasance yana ɗora tafin hannayensa ne a kan gwiwarsa, da kuma buɗa tsakanin 'yan yatsunsa. Ga wasu daga cikin kurakuran da suka yawaita a tsakankanin masallata, da kuma abin da yake shi ne daidai:

- Ɗora hannu a cinya ko ƙwauri, wanda yin hakan kuskure ne, abin da yake daidai shi ne ɗora su a kan cinya, kamar yadda hadisi ya zo wajen bayyana siffar sallar Manzon Allah tsira da amincin Allah su ƙara tabbata a gare shi "*yana ɗora hannayensa a kan cinyoyinsa*".

- Liƙa gwiwar hannunsa da jikinsa: Shi ma wannan kuskure ne da masallata suke yi yayin ruku'u, domin hakan yana kai mutum ya takure kansa da rashin yin Sallah a cikin nutsuwa.
- Durƙufar da gadon baya: shi ne mutum ya sunkuyar da kansa ƙasa, kamar zai gangaro, ko kuma kamar zai ɗau wani abu, wanda shi ma yin haka kuskure ne a cikin siffar ruku'u. Abin da yake daidai shi ne mutum ya daidaita bayansa kar ya takure, kamar yadda Annabi tsira da amincin Allah su ƙara tabbata a gare shi yake yi "*Idan zai yi ruku'u yana miƙar da gadon bayansa, kuma ya daidaita shi*"
- Cusa kai tsakanin cinyoyi: Kuskure ne da ake yi yayin ruku'u, ta yadda wasu daga cikin masallata suke cusa kawunansu (watau sunkuyar da kawunansu kamar masu leƙa wanda ke bayansu ta tsakankanin cinyoyinsu) a cinyoyinsu yayin ruku'u. Annabi tsira da amincin Allah su ƙara tabbata a gare shi ya kasance "*Ba ya sunkuyar da kansa, kuma ba ya ɗagawa, sai dai ya kasance a tsaka-tsaki (shi ba ɗagowa ba, kuma ba sunkuyarwa ba*".
- Haɗe karatun Sallah da kabbarar ruku'u: Shi ma wannan wani kuskure ne da ya yaɗu a tsakanin masallata; musamman limaman da suke jan Sallah, ta yadda ba sa yin shiru na ɗan lokaci bayan gama karatun kafin tafiya ruku'u ba, wanda hakan abu ne da ya saɓa wa koyarwarsa tsira da amincin Allah su ƙara tabbata a gare shi. Abin da yake daidai wajen koyi da Sunnar Manzon Allah tsira da amincin Allah su ƙara tabbata a gare shi, shi ne yin shiru na wani lokaci bayan kammala karatun Sallah gabaɗaya (kafin ruku'u).
- Yin ruku'u kafin liman: Rigayar liman wajen yin ruku'u shi ma abu ne da ya yaɗu a tsakanin masallata, wanda yin hakan kuskure ne, kuma Manzon Allah tsira da amincin Allah su ƙara tabata a gare shi yayi hani da hakan inda yake cewa, "*Ya ku mutane, lallai ni ina gabanku kada ku rigaye ni da yin ruku'u ko da sujjada, ko da tsaiwa, ko da sallamewa*".

- Karanta Alƙur'ani a yayin ruku'u: Yin haka a yayin ruku'u ko a cikinsa kuskure ne, Manzon Allah tsira da amincin Allah su ƙara tabbata a gare shi kuma yayi hani da hakan, yake cewa: "*Ku saurara lallai an hane ni da karanta Alƙur'ani (alhalin ina) mai ruku'u ko sujjada, amma (a cikin) ruku'u ku girmama Allah mabuwayi, amma sujjada ku yawaita addu'a.*" Imamun Nawawi ya ce: (A cikin hadisin), akwai hani wajen karanta Alƙur'ani a cikin ruku'u da sujjada, abin sani aikin da ake yi a cikin ruku'u shi ne tsarkake Allah, a sujjada kuma tsarkake shi da roƙonsa". Wannan yake bayyana cewa *azkar* ake yi yayin ruku'u. waɗannan *azkar* kuwa suna da yawa; sai dai mutum zai iya yin gwargwadon wacce ya iya, wasu daga cikin waɗannan *azkar* su ne:

***Subhana Rabbiyal azim*** "سُبْحَانَ رَبِّيَ العَظِيمِ" Ana faɗar wannan ne daga ɗaya zuwa abin da ya sawwaƙa, Sayyid Sabiƙ ya faɗa a cikin Fiƙihus sunna: "*Duk wanda ya yi Tasbihi sau goma, to, ya yawaita.*" Sai kuma wata addu'ar, ***Subhanakal Lahumma Rabbana wa bi Hamdika Allahummagh fir li*** "سُبْحَانَكَ اللَّهُمَّ رَبَّنَا وَبِحَمْدِكَ اللَّهُمَّ اغْفِرْ لِي" Wannan addu'a Annabi tsira da amincin Allah su ƙara tabbata ya kasance yana yawan karanta ta a cikin ruku'u, kamar yadda hadisi ya zo daga mahaifiyar muninai Aisha Allah ya ƙara mata yarda
Daga cikin wata addu'ar dai ta ruku'u akwai:

"*Allahumma laka raka'atu, wa bika amantu, wa laka aslamtu, khasha'a laka sam'i, wa basari, wa mukhii, wa azamii, wa asabi"*

**(اللهُمَّ لَكَ رَكَعْتُ، وَبِكَ آمَنْتُ وَلَكَ أَسْلَمْتُ، خَشَعَ لَكَ سَمْعِي، وَبَصَرِي، وَمُخِّي، وَعَظْمِي، وَعَصَبِي)**

Ita ma wannan addu'a Manzon Allah tsira da amincin Allah su ƙara tabbata a gare shi ya kasance yana yin ta a cikin ruku'u. Idan ya ɗago kuma yana cewa:

'*Sami Allahu liman hamida hu.'*

*'Allahumma Rabbana lakal hamdu, mil'as samawati wa mil'ar ardhi wa mil'a ma baina huma, wa mil'a ma shi'ita min shai'in ba'adu.'*

(سَمِعَ اللهُ لِمَنْ حَمِدَهُ)

( اللهُمَّ رَبَّنَا لَكَ الْحَمْدُ مِلْءَ السَّمَاوَاتِ، وَمِلْءَ الأَرْضِ، وَمِلْءَ مَا بَيْنَهُمَا، وَمِلْءَ مَا شِئْتَ مِنْ شَيْءٍ بَعْدُ)

Waɗannan su ne wasu daga cikin addu'o'in da ake yi yayin ruku'u, kuma yana daga cikin abin da ake so masallata su kiyaye wajen ruku'u shi ne daidaituwa, da kuma tsawaitawa ta yadda mutum zai girmama Ubangiji a cikin nutsuwa da kushu'i.

Ya kai ɗan'uwa mai albarka ka sani cewa, duk lokacin da ka karɓi wani gyara a cikin wannan addini na Musulunci, to, ka turmutsa hancin Shaiɗan kuma ka hau hanyar da Allah yake so bawansa ya kasance, Allah ya datar da mu.

3.5 Kurakuran Sujjada

Kamar yadda ake wasu kurakurai a yayin ruku'u, saboda mantuwa ko rashin sani, wanda hakan har ya zamanto kamar ɗabi'ar mafi yawan gama-garin masallata. Da akwai waɗansu kurakuran dai da ake yi kuma suka yaɗu a yayin sujjada, daga cikin waɗannan kurakurai su ne:

- Rashin daidaita gaɓoɓin da ake yin sujjada da su a wajen da mutum zai yi sujjadar: Da akwai gaɓoɓi guda bakwai waɗanda Annabi Mai tsira da aminci yake cewa : An umarce ni da na yi sujjada a kan gaɓoɓi guda bakwai: Hanci, da hannaye, da gwiwoyi, da ƙafafu".
- Ɓarin addu'a a cikin sujjada.
- Shimfiɗa tsintsiyar hannu, da matse hammata.
- Rashin nutsuwa a cikin sujjada.
- Yin sujjada a bisa tufafin jikinsa ko gashi.
- Kuskure wajen siffar zama tsakanin sujjadu biyu.
- Kuskure wajen barin addu'o'i tsakanin sujjadu biyu.

- Kuskure wajen inkarin zaman hutu (Jalsatul Istiraha). Duk da cewa bai kamata a gwama numfashi akan wannan ba, domin mallamai sun yi bayanan da suke nuna yin sa da rashin yin sa ba zai cutar ba sam. Allah shi ne mafi sani.
- Kuskure wajen karanta Alƙur'ani a cikin sujjada.
- Ɗora gwiwoyi kafin hannaye yayin da za a tafi sujjada.
- Ɗaga wani abu domin yin sujjada a kansa.
- Yin sujjada a kan gefen ragowar rawani.

Ya kai ɗan'uwa mai albarka ka sani cewa, duk lokacin da ka karɓi wani gyara a cikin wannan addini na Musulunci, to, ka turmutsa hancin Shaiɗan kuma ka hau hanyar da Allah yake so bawansa ya kasance, Allah ya datar da kai.

### 3.6 Kurakuran Sallama Da Bayan Sallama

Da akwai wasu kurakurai da mafi yawan masallata suke yi, yayin Sallama, ko kuma bayan sun yi Sallama daga Sallah, waɗannan kurakurai su ne:

- Juya hannaye yayin Sallama: Manzon Allah tsira da amincin Allah su ƙara tabbata a gare shi, ya yi hani ga hakan, kamar yadda ya zo a cikin hadisi wanda Jabir ɗan Samura Allah ya ƙara masa yarda ya rawaito: "Mun kasance idan za mu yi Sallah tare da Manzon Allah tsira da amincin Allah su ƙara tabbata a gare shi, sai mu ce: *Assalamu Alaikum Wa Rahamatullah, Assalamu Alaikum Wa Rahamatulla*, sai (Jabir) yayi nunin Sallamar guda biyu da hannunsa, sai Manzon Allah tsira da amincin Allah su ƙara tabbata a gare shi ya ce: Me ya sa kuke ɗaga hannayenku, ba za ku tsayar da su ba, ya ishi ɗayanku kawai ya ɗora hannunsa a kan cinyarsa; sannan sai yayi Sallama ga ɗan'uwansa da (yake) ɗangaren damansa da hagunsa".
- Faɗin wannan addu'a ta: '*Allahumma adkilnal jannata, wa as'alukan najata minan nar'* (اللهم أدِخلنا الجنَّة، وأسألكَ النَّجاة من النار), yana daga cikin kurakuran da suka yaɗu a wajen maSallahta da yawa. Sheik Mahfuz ya ce: Yana daga cikin bidi'a abar ƙyama

(wajen) faɗin mai Sallah bayan Sallamar farko: Allah ka shigar da ni aljanna, bayan ta biyu kuma: Ina neman tsarinka daga wuta, wasu daga cikin malamai suka ce: Wannan abu ne da Annabi tsira da amincin Allah su ƙara tabbata a gare shi bai aikata ba, ko wani daga cikin malamai, ƙirƙirarren abu ne a cikin Sallah a wajen da ba gurbinsa ba, yana rabe ɗaya daga cikinsu, tsakanin Sallama guda biyu, ya haɗe ɗayar kuma da Sallama ta biyu, babu wani da yake da ikon raba siffar da aka shara'anta da irin wannan.

- Gaisawa kai tsaye bayan Sallama: Yana daga cikin kurakuran da ake yi bayan Sallama shi ne, gaisawa kai tsaye bayan idar da Sallah, wannan shi ma abu ne wanda babu shi a cikin siffar Sallar Annabi tsira da amincin Allah su ƙara tabbata a gare shi, kuma babu wani daga cikin sahabbai da aka samu ya yi irin aikin.

Izzu bin Abdussalam ya ce: *Gaisawa bayan Sallar Asuba, da La'asar, suna daga cikin ƙirƙirarrun abubuwa, sai dai ga mutumin da ya zo ya haɗu da wanda zai gaisa da shi kafin Sallah.*"

- Bayyana Tasbihi da Istigfari cikin mutane a tare: Wannan kurakurai ne da mutane suka samar da su, har ya zamo sun yaɗu kamar duhun dare. Istigfari da murya ɗaya a cikin jama'a bayan Sallama, da faɗin mutane: "*Ya Arrahamar-rahimina Irhamna*", da karanta Ayatul Kursiyyu da murya ɗaya ta yadda wanda yake maƙotaka da masallacin yana ji".
- Addu'a kai tsaye bayan Sallama: Waɗansu daga ciki suna barin sunna; shi ne addu'a yayin sujjada, sai su aikata bidi'a, shi ne yin addu'a kai tsaye bayan Sallama. Manzon Allah tsira da amincin Allah su ƙara tabbata a gare shi bai aikata hakan ba, haka ma sahabansa, Allah ya ƙara masa yarda".

Sheikul Islam Ibnu Taimiyya, *rahimahullahu,* ya ce: " Ba a samu ba cewa Annabi tsira da amincin Allah su ƙara tabbata a gare shi idan ya sallaci mutane yana yi musu addu'a bayan idar da Sallah shi da waɗanda suke bin sa ba gabaɗaya, a Sallahr Alfijir ce ko waninta,

ko Sallar La'asar ko wasu daga cikin salloli. Abin sani kawai ya tabbata daga shi; yana fuskantar sahabansa bayan idar da Sallah, kuma ya ambaci Allah ya koyar da su addu'o'i bayan idar da Sallah. Kuma a kan wannan zance Ibnul Kayyum ya tafi, a cikin litatfinsa Zadul ma'ad".

- Yin sujjada domin addu'a bayan idar da Sallah: Ya zamo ɗabi'a da ala'dar wasu masallatan ta wajen yin sujjada bayan liman ya yi Ssallama (watau bayan liman ya idar da Sallarsa; sai wasu daga cikin masu bin liman ɗin su yi sujjada, wanda hakan zai rikirkitar da wasu, har su zata ko sujjada ba'adi ce).

Ya kai ɗan'uwa mai albarka ka sani cewa, duk lokacin da ka karɓi wani gyara a cikin wannan addini na Musulunci, to, ka turmutsa hancin Shaiɗan kuma ka hau hanyar da Allah yake so bawansa ya kasance, Allah ya datar da kai.

## 3.7 Wasu Daga Cikin Kurakuren Da Ba a Ɗauke Su a Matsayin Kuskure Ba

1. Barin wayar hannu ba tare da an saka ta a cikin shiru ko ma a kashe ta, don girman muhimmancin salla.
2. Gaggawar tashi da zarar liman yayi sallama ba tare da uzuri karɓaɓɓe ba, abin da ya kamata a wannan lokacin gabatar da zikirorin da ma'aikin Allah ya karantar (S.A.W).
3. Kin ɗagowa daga sujjada bayan liman ya ɗago da sunan addu'a ake, hakan ba shakka saɓa wa shari'a ne, shi liman an saka shi ne don a yi koyi da shi, in ya yi a yi ba tare da jinkiri ko ƙari ba.
4. Lazimtar yin sallar raka'atanilfajri bayan sallar asuba, wannan ta kai har wasu sun ɗauka hakan shi ne sunnah! Alhali hakan saɓa wa sunna ne matukar ba uzuri karɓaɓɓe! Domin lokacinta da shari'a ta tanadar shi ne bayan ketowar alfijir, kafin sallar asuba.
5. Rashin daidaita sahu da kyau, da ɗora hannu a ƙasan cibiya ko ƙasan wuya da soshe-soshen gemu ko gashi, da duk wani motsin da zai rage cikakkiyar nutsuwa a cikin rukunai ko sunnonin sallah.

6. Taɓe-taɓen waya ko *chatting* yayin da liman yake huɗuba, Ranar Juma'a, wanda abin da yake wajibi shi ne a daidai wannan lokacin masallaci ya bar komai ya saurari huɗuba daga liman.
7. Karatun Kur'ani da ɗaga murya yayin zaman jiran zuwan liman kafin Sallar Juma'a, musamman a lokacin da ake gabatar da wata 'yar faɗakarwa kafin zuwan liman, wadda aka fi sani da *pre-khuɗuba,* abin da ya fi dacewa a daidai wannan lokacin shi ne sauraron wannan faɗakarwar, in kuma ba haka ba, to mutum ya gabatar da ibadarsa ta karatu ko wasu zikirai ta yadda ba sai ya ɗaga murya ya cutar da mai gabatar da faɗakarwar ko na kusa da shi ba.
8. Zuwa da yaro masallaci,yana daga cikin kuskuren da masallata suke yi., da sunan tarbiyantar da yaya, wanda hakan yana kaiwa ga gushewar nutsuwa a sallah, saboda wasannin da yaro zai yi.
9. Kin fitowar masallaci sallah, har sai ya ji an tayar da iƙama! Sa'annan ya fito yana sauri-sauri gudu-gudu, hakan sai ya zama laifikan laifi.

Ya kai ɗan uwa mai albarka kayi hakuri ka karɓi gyara baka da wani abin da ya kai bauta wa Allah irin yadda yake son a bauta masa, don ya halicce ka ne dalilin ka bauta masa.

# 4.0 FASALI NA HUƊU

Wannnan fasali zai yi Magana ne game da wasu maganganun magabata game da sallah kamar:

4.1 Maganganun Malamai a Game Da Sallah a Gaban Limaman
4.2 Haƙiƙanin Siffar Sallar Annabi (S.A.W).
4.3 Bayanin Malamai a Kan Sallar Annabi (S.A.W).
4.4 Tasirin Yin Irin Sallar Annabi (S.A.W).
4.5 Hatsarin Saɓa Wa Sallar Annabi (S.A.W).
4.6 Kammalawa
4.7 Jerin Litattafan Da Aka Duba

## 4.1 Maganganun Malamai a Game Da Sallah a Gaban Limaman

Abubakar Annaisaburi ya ce: "Manzon Allah tsira da amincin Allah su ƙara tabbata a gare shi ya sunnanta cewa limami ya zamo a gaban masu bin Sallah. Malamai ma'abota ilimi sun yi saɓani game da mai bin limanin da ya yi Sallah a gaban liman saboda halin larura na cunkoso ko makamancin haka. Sai wasu jam'a suka ce: Idan Sallar mai bin liman a gabansa ta zamanto saboda waɗancan larurori da aka ambata ne, to, Sallar ta halatta. Wannan shi ne faɗin Imamu Malik idan aka samu cunkoson sahu a Sallar Juma'a. Wasu jama'ar kuma suka ce: Ba ya halatta mai bin liman yayi Sallah a gaban limaminsa, wannan kuma shi ne faɗin Imamush-shafi'I, Allah ya yi musu Rahama". Amin.

Sheikhul Islam bin Taimiyya ya ce: "Sallah a gaban liman tana halatta, idan da wata larurar, kamar tsananin cunkoso, misalin ranar Juma'a, ko kamar yadda yake faruwa a Mina a masallacin Da'if, haƙiƙa mutane suna Sallah a gaban liman ma'ana a wajen masallacin, amma wannan saboda uzuri ne; sai dai dole ya zamanto sahun ya haɗe".

Ya kai ɗan'uwa mai albarka ka sani cewa, duk lokacin da ka karɓi wani gyara a cikin wannan addini na Musulunci, to, ka turmutsa hancin Shaiɗan kuma ka hau hanyar da Allah yake so bawansa ya kasance, Allah ya datar da kai.

## 4.2 Haƙiƙanin Siffar Sallar Annabi (S.A.W).

Annabi tsira da amincin Allah su ƙara tabbata a gare shi ya kasance yana yin Sallar nafila da ta farilla a tsaye, amma a halin tafiya kuwa yana yin Sallar nafilarsa a kan abin hawansa.

Sannan ya kasance yana ɗaga hannuwansa wani lokacin tare da kabbara; wani lokacin kuma bayan kabbara; wani lokacin kuma kafin kabbara, kuma ya kasance yana ɗaga hannayensa, tare da miƙar da yan yatsunsa, ba ya ware su, kuma ba ya haɗe su.

Daga cikin siffar Sallarsa tsira da da amincin Allah su ƙara tabbata a gare shi, ya kasance yana ɗora hannunsa na dama a kan na hagu, kuma ya kasance yana cewa: "An umarce mu, ɗokacin Annabawa, da mu gaggauta buɗa-baki (shan ruwa bayan faɗuwar rana), kuma mu jinkirta sahur, kuma mu ɗora hannayen damanmu a kan hagu (yayin) da muke cikin Sallah. Haka Anabi tsira da amincin Allah su ƙara tabbata a gare shi ya wuce wani mutum yana Sallah ya ɗora hannunsa na hagu a kan dama, sai ya cire hannun ya ɗora damar a kan hagu. Haka Annabi tsira da amincin Allah su ƙara tabbata a gare shi ya kasance idan zai yi Sallah sai ya sunkuyar da kansa, ya tsayar da ganinsa wajen da zai yi sujjada, saboda haka yana daga cikin siffar Sallar Annabi, idan mutum zai yi Sallah ya kalli wajen da zai yi sujjada, sai lokacin tahiya da zai kalli gefen ɗanyatsansa, domin kar ya kalli wani wajen ya shagaltu da wani abin. Kamar yadda Annabi tsira da amincin Allah su ƙara tabbata a gare shi yayi hane mu da kallon sama yayin da muke Sallah.

Daga Abu Humaid Assa'idi, Allah ya ƙara masa yarda, yayin da yake hakaito siffar Sallar Annabi tsira da amincin Allah su ƙara tabbata a gare shi ya ce: "Lallai ni na fiku kiyaye Sallar Manzon Allah tsira da amincin Allah su ƙara tabbata a gare shi, na gan shi idan zai yi kabbara sai ya sa hannunsa daidai kafaɗarsa, idan zai yi ruku'u sai ya sa hannunsa a kan gwiwoyinsa, sannan ya miƙar da bayansa, idan ya ɗago kansa (daga ruku'u) sai ya daidaita; har (ƙashin kowacce gaɓa) ya koma wajensa (ya miƙe), idan ya yi sujjada kuma sai ya ɗora tafukan hannunsa, ba tare da shimfiɗe su

ba, ko dunƙule su ba, sai gefen 'yan yatsun ƙafarsa su kalli alƙibila; idan zai zauna a raka'o'in sujjada ta biyu sai ya zauna a kan ƙafarsa ta hagu, kuma ya kafe ta dama, idan zai zauna a raka'ar ƙarshe, (watau tahiyar ƙarshe), sai ya gabatar da ƙafarsa ta hagu (wato yana zuro ƙafarsa ta hagu ta ƙarƙashin ƙwaurinsa na dama), sai ya kafe ta dama".

Daga Zubairu ɗan Awwam, Allah ya ƙara masa yarda ya ce: " Manzon Allah tsira da amincin Allah su ƙara tabbata a gare shi ya kasance idan ya zauna yana yin tahiya; sai ya ɗora hannunsa na dama a kan cinyar dama, da hannunsa na hagu a kan cinyar hagu, sai yayi nuni da manuniyar ɗan yatsansa, kuma sai ya ɗora babban ɗan'yatsansa a kan (ɗan'yatsan) tsakiya, ya shimfiɗa tafin hannunsa na hagu a kan cinyarsa".

Sannan ya kasance yana buɗe karatunsa da addu'o'i mabambanta masu yawa, (waɗanda) yake gode wa Allah Maɗaukaki a ciki, ya gode masa kuma ya yabe shi, sannan ya yi umarni da haka. Sannan ya kasance yana neman tsarin Allah maɗaukaki (a yayin da zai fara karatun Sallah), sai ya ce:

'*A'uzu bil Lahi minash shaiɗanir rajiym, min hamzhihi wa nafkhihi wa nafthihi.*"

**(أَعُوذُ بِاللَّهِ مِنَ الشَّيْطَانِ الرَّجِيمِ مِنْ هَمْزِهِ وَنَفْخِهِ وَنَفْثِهِ)**

Wani lokacin kuma ya ƙara sai ya ce:

"*A'uzu bil Lahis Sami'il Aliym minash shaiɗanir rajiym, min hamzhihi, wa nafkhihi wa nafthihi.*"

**(أَعُوذُ بِاللهِ السَّمِيعِ الْعَلِيمِ مِنَ الشَّيْطَانِ الرَّجِيمِ، مِنْ هَمْزِهِ، وَنَفْخِهِ، وَنَفْثِهِ)**

Sannan sai ya karanta
"*Bismillahir Rahmanir Rahiym.*" **(بِسْمِ اللهِ الرَّحْمَنِ الرَّحِيمِ)**
ba tare da ya bayyana ta ba".

Daga cikin abin da yake ƙara bayyana cewa Annabi tsira da amincin Allah su ƙara tabbata a gare shi yana buɗe Sallarsa da addu'a shi ne, hadisin da Abu Huraira Allah ya ƙara masa yarda ya rawaito, inda

yake tambayar Annabi tsira da amincin Allah su ƙara tabbata a gare shi yake cewa "Manzon Allah ya kasance idan ya yi kabbarar haramar tayar da Sallah sai ya yi shiru, kafin ya fara karatu, sai na ce  da shi: Mahaifina da mahaifiyata fansa ne a gare ka; ba ni labarin abin da kake faɗa game da shirun da kake yi tsakanin kabbara da karatu, sai Manzon Allah tsira da amincin Allah su ƙara tabbata a gare shi ya ce, ina cewa :

**(اللَّهُمَّ بَاعِدْ بَيْنِي وَبَيْنَ خَطَايَايَ كَمَا بَاعَدْتَ بَيْنَ الْمَشْرِقِ وَالْمَغْرِبِ، اللَّهُمَّ نَقِّنِي مِنَ الْخَطَايَا كَمَا يُنَقَّى الثَّوْبُ الأَبْيَضُ مِنَ الدَّنَسِ، اللَّهُمَّ اغْسِلْنِي مِنْ خَطَايَايَ بِالْمَاءِ وَالْبَرَدِ وَالثَّلْجِ)**

"Ya Allah! ka nisanta tsakanina da laifukana, kamar yadda ka nisanta tsakanin gabas da yamma, Ya Allah! Ka tsarkake ni daga laifukana, kamar yadda ake tsarkake farar tufafi daga ƙazanta, Ya Allah! Ka wanke ni daga laifukana, da ƙanƙara da ruwa da raɓa".

Mahaifiyar Muminai Aisha Allah ya ƙara mata yarda take siffanta Sallar shugaban halittu, take cewa: "Manzon Allah tsira da amincin Allah su ƙara tabbata a gare shi ya kasance yana buɗe Sallarsa da kabbara; da karatu; da godiyar Ubangiji, ya kasance idan zai yi ruku'u ba ya ƙasa da kansa, kuma ba ya ɗago shi; sai dai ya kasance yana tsaka-tsaki (wajen daidaita shi da gadon bayansa), ya kasance idan ya ɗago daga ruku'u ba ya tafiya sujjada har sai ya daidaita a tsaye, idan ya ɗago kansa daga sujjada kuma, ba zai yi wata sujjadar ba; har sai ya daidaita a zaune, ya kasance yana yin tahiya a kowacce raka'a biyu, kuma yana shimfiɗa ƙafarsa ta hagu ya kafe ta dama. Ya kasance yayi hani da gurfanon Shaiɗan (wato bubbuɗe dugadugan hagu da na dama ta yadda mazaunai za su taɓa ƙasa kai tsaye), kuma ya yi hani mutum ya shimfiɗa hannunsa (irin shimfiɗawar kare, da wasu dabbobi irinsa masu fiƙa kamar damisa ko kyanwa….), kuma ya kasance yana gama Sallarsa da Sallama".

Daga cikin siffar Sallarsa, tsira da amincin Allah su ƙara tabbata a gare shi, ya kasance yana karanta aya dalla-dalla, ɗaya bayan ɗaya a cikin Sallah.

Yana karanta Suratul Fatiha aya-aya kamar haka:
"*Bismillahir Rahmanir Rahiym"*

**(الْحَمْدُ للهِّ رَبِّ الْعالَمِينَ)**

Sai ya tsaya, sa'annan ya ɗora da, "*Alhamdu lillahi Rabbil Alamiyn."* Sai ya cigaba a haka yana ɗan tsahirtawa a ƙarshen kowacce aya har zuwa ƙarshen Fatiha, haka ma Sura; kamar yadda zai zo a gaba dalla-dalla.
Sai dai ba ya bayyana Bisimilla a farko, kamar yadda babban sahabi Anas ɗan Malik Allah ya ƙara masa yarda yake cewa: "Na yi Sallah tare da Annabi da Abubakar, da Umar da Usman (amma) ban taɓa sani daga cikinsu, karanta Bisimilla a (fili ba).
Bayan Annabi tsira da amincin Allah su ƙara tabbata a gare shi ya karanta Basmala, sai ya tsaya, sannan ya karanta:

**( الْحَمْدُ للهِّ رَبِّ الْعالَمِينَ)**

Sannan sai ya sake tsayawa, sai ya ƙara faɗi:

**(الرَّحْمنِ الرَّحِيمِ)**

Sannan sai ya sake tsayawa, sai ya ƙara faɗin:

**(مالِكِ يَوْمِ الدِّين)**

Sannan sai ya sake tsayawa, sai ya ƙara faɗin:

**(إِيَّاكَ نَعْبُدُ وَإِيَّاكَ نَسْتَعِينُ)**

Sannan sai ya sake tsayawa, sai ya ƙara faɗin:

**(اهْدِنَا الصِّراطَ الْمُسْتَقِيمَ)**

Sannan sai ya sake tsayawa, sai ya ƙara faɗin:

**(صِراطَ الَّذِينَ أَنْعَمْتَ عَلَيْهِمْ غَيْرِ الْمَغْضُوبِ عَلَيْهِمْ وَلا الضَّالِّينَ)**

Haka Manzon Allah Mai tsira da aminci yake karanta Fatiha, yana tsayawa a kan gundarin ayar ba tare da ya haɗe da wacce take gabanta ba (daki-daki), ko da ma'anarsu tana da alaƙa da juna.
Sannan sai ya yi shiru idan ya gama karatun Sallah, sai ya ɗaga hannayensa, sai ya yi kabbara da ruku'u, yadda yake yin ruku'u kuwa shi ne:

- Zai ɗora hannayensa a kan gwiwoyinsa, tare da buɗe tsakanin yan'yatsunsa yana mai damƙe gwiwoyinsa.

- Yana miƙar da gadon bayansa; ta yadda da za a zuba ruwa a bayansa (gadon bayan) da ruwan ya zauna (ma'ana bai gangaro ya kwaranyo ba, saboda yadda ya daidaita). Daga Abu Mas'ud Allah ya ƙara masa yarda ya ce, lallai Manzon Allah tsira da amincin Allah su ƙara tabbataa gare shi ya ce: "Babu Sallah ga wanda bai miƙar da gadon bayansa (daidaita shi ba) a cikin ruku'u da sujjada".
- Ba ya sunkuyar da kansa (ƙasa sosai), kuma ba ya ɗaga shi, sai dai tsaka-tsaki wajen daidaita shi da gadon bayansa.
- Ya kasance yana nutsuwa da daidaituwa a cikin ruku'insa, kuma ya umarci musulmai da su aikata haka inda yake cewa: "*Ku cika ruku'u da sujjada, lallai ni ina ganinku ta bayana, idan kuka yi ruku'u da yayin da za ku yi sujjada*".
- Ya kasance yana daidaita ruku'unsa, da tsayuwarsa bayan ruku'u da zamansa tsakanin sujjadu biyu, kusan kai-ɗaya.
- Yana ɗagowa daga ruku'u a nutse, har sai kowacce gaɓa ta koma muhallinta.
- Yana sanya kusan daɗewarsa a tsaye ta kusa da wacce ya yi a ruku'u, har sahabansa tsira da aminci suna cewa: "Wani lokacin yana tsayawa, har sai mutum ya ce ko ya manta ne, saboda daɗewar da ya yi a tsaye"

Amma yadda yake sujjadarsa kuwa shi ne:

- Yana yin kabbara, wato faɗin *Allahu Akbar* (الله أكبر)
- Yana ɗaga hannayensa kusa da kafaɗarsa a yayin kabbarar harama, wani lokacin tare da kabbarar, wani lokacin kuma sai bayan yayi kabbarar sai ya ɗaga hannun, kuma ba ya tattale su ko gwama su a waje ɗaya.
- Yana ɗora hannayensa a ƙasa kafin gwiwoyinsa (ma'ana shi ne ba gwiwoyinsa ne suke fara zuwa ƙasa ba, yayin da zai tafi sujjada) domin hakan durƙuson raƙuma ne, kuma Annabi tsira da amincin Allah su ƙara tabbata a gare shi yayi hani ga hakan, inda yake cewa: "Kar ɗayanku yayi gurfano kamar yadda

raƙumi yake yi, (abin da zai yi shi ne) ya ɗora hannayensa kafin gwiwoyinsa".

- Yana shimfiɗa tafukan hannunsa yayin sujjada ya miƙar da su, da fuskantar da su ga alƙibila.
- Yana sanya tafukan hannunsa daf da kafaɗunsa, wani lokacin kuma kusa da kunnuwansa, kuma yana nesanta tsintsiyar hannunsa da ƙasa, yana cewa "kar ɗayanku ya shimfiɗa hannunsa (a ƙasa yayin Sallah), irin yadda kare yake yi"
- Yana haɗa hancinsa da goshinsa a ƙasa, (suna taɓa ƙasa), haka ma gwiwoyinsa da gefen ƙafafuwansa, tare da kafe su da fuskantar da yan yatsunsa ga alƙibila.
- Yana daga cikin siffar Sallarsa tsira da aminci su ƙara tabbata a gare shi, yin sujjadar a nutse tare da daidaituwa, kuma daɗewa a sujjadarsa tana kusa da daɗewarsa a lokacin ruku'u.
- Idan ya ɗago daga sujjada ba ya tafiya wata har sai kowacce gaɓa ta koma muhallinta, sannan yana shimfiɗa ƙafar hagu ya zauna a kanta, ta dama kuma ya kafe ta, kuma yana tsawaita zamansa bayan ya ɗago daga sujjada, har ya zamanto kusa da (irin daɗewar da yayi) a sujjadarsa.
- Ya kasance yana yin zaman hutu a cikin Sallah (*Jalsatul Istiraha*).

Annabi tsira da amincin Allah su ƙara tabbata a gare shi ya kasance idan zai yi Sallahma a Sallarsa, yana farawa ne da damansa ta yadda yake cewa:

"*Assalamu Alaikum wa Rahmatul Lah*" (السلام عليكم ورحمة الله)

Bayan ya yi wannan a ɓangaren damansa, sai kuma ya sake yin wata Sallamar a ɓangaren hagun ɗinsa:
Wani lokacin kuma yakan fara sallamar da irin wannan sigar:

"*Assalamu Alaikum wa Rahmatul Lahi wa Barakatuhu*"

(السَّلاَمُ عَلَيْكُمْ وَرَحْمَةُ اللهِّ وبركاته)

a damansa, sa'annan kuma a hagun ɗinsa sai ya karanta:

"*Assalamu Alaikum wa Rahmatul Lah"* (السَّلاَمُ عَلَيْكُمْ وَرَحْمَةُ اللهِ)

Ba tare da ya ƙara da *wa barakatuhu* ba.

Wani lokacin kuma yana yin Sallamarsa da:

(السَّلاَمُ عَلَيْكُمْ وَرَحْمَةُ اللهِ)

A ɓangaren damansa, sai kuma a ɓangaren hagunsa ya ce:

(السَّلاَمُ عَلَيْكُمْ )

Wani lokacin kuma yana yin Sallama guda ɗaya ne, yana mai karkatar da fuskarsa ga damansa. (Kamar yadda Mazhabar Malikiyya suka ɗauki wannan).
Wannan shi ne siffar yadda Manzon Allah tsira da amincin Allah su ƙara tabbata a gare shi yake Sallarsa.

4.3 BAYANIN MALAMAI A KAN SALLAR ANNABI (S.A.W).
Daga Huzaifatu ɗan Yaman. Allah ya ƙara masa yarda ya ce: "Wata rana nayi Sallah a bayan Annabi tsira da amincin Allah su ƙara tabbata a gare shi, sai ya fara karanta suratul Baƙara (bai tsaya ba) sai na ce (wataƙila) zai yi ruku'u a daidai aya ta ɗari, sai ya wuce (bai tsaya ba), sai na ce (to, wataƙila) duk zai gama ta a raka'a ɗaya ne, sai ya wuce, sai na ce (wataƙila) zai yu ruku'u da ita, sannan sai ya shiga suratun Nisa'i ya karanta ta (gabaɗaya), ya shiga Al Imrana ya karanta ta. Yana karatu daki-daki (dalla-dalla), idan ya wuce ta ayar da take ambaton Allah (shi ma) sai ya ambace shi, idan ya wuce ta tambaya kuma sai yayi tambaya, idan ya wuce ta neman tsari kuma sai ya nemi tsari, sannan sai yayi ruku'u sai ya ce ( سبحان ربي العظيم), kuma ruku'unsa ya kasance kwatankwacin tsaiwarsa, idan ya ɗago sai ya ce, (سمع الله لمن حمده), sannan sai ya daɗe a tsaye kwatankwacin daɗewar da yayi a ruku'u, sannan sai ya yi sujjada (sai ya ce a cikin sujjadar), (سبحان ربي الأعلى), kuma (daɗewarsa) a cikin sujjada kusa da kwatankwacin wacce ya yi a tsayuwarsa".
Yahaya bin Hubaira ya ce game da wannan hadisi: "A cikinsa da akwai halaccin tsawaita Sallah, idan ta nafila ce mutum (zai iya

tsawaitawa) a karankansa, ko ga wanda ya san zai iya jure (tsaiwar) a tare da shi, amma Sallar farilla kuwa an fi so ya taƙaita, tare da cika ruku'unta da sujjadarta".
Imamun Nawawi ya ce: "A cikin hadisin da akwai dalili ga waɗanda suke cewa jera karatun sura a cikin Sallah ijtihadi ne daga musulmai, lokacin da za a tattara Alƙur'ani a littafi ɗaya (Mushaf)".
Faisal bin Abdul'aziz bin Faisal ya ce: "A cikin hadisin da akwai wajibcin tsawaitawa a dukkanin rukunai a Sallar dare".
Ahmad bin Abdurrahman bin Muhammad Bunna ya ce: "Babu saɓani a kan cewa idan mai Sallah ya karanta surar da take kafin wacce ya karanta a raka'a ta biyu".
Sheikh Usaimin ya ce: " Sai Manzon Allah tsira da amincin Allah su ƙara tabbata a gare shi ya tattara (abubuwa a cikin Sallarsa) tsakanin karatu, da ambaton Allah, da addu'a da tunanin (abin da yake karantawa, wajen bibiyar ma'anoni), saboda wanda yake tambaya a yayin tambaya, kuma yake neman tsari a yayin neman tsari, kuma yake Tasbihi a wajen tasbihi, (lallai) babu shakka yana lura a cikin karatunsa, kuma yana tun-tun-tunin abin da yake karantawa, sai wannan tsayuwar ta zamo wani dausayi ne, na ambaton Allah (wajen) yin karatu da tasbihi, addu'a, da tun-tun-tuni, (kuma) dukkanin waɗannan abubuwa Annabi tsira da amincin Allah su ƙara tabbata a gare shi yayi su a raka'a ɗaya, ba tare da yayi ruku'u ba, ya karanta Baƙara, da Nisa"i da Al'imran, sama da juzu'i biyar da kwata (izu goma da ɗoriya), idan mutum yana irin wannan karatu a hankali, kuma yana neman tsari a wajen narkon azaba, kuma ya nemi (rabauta) a ayar da take (maganar) Rahama, kuma ya ambaci Allah a wajen ambatonsa, tsawon wane lokaci Sallarsa za ta ɗauka? Babu shakka (irin) wannan Sallahr za ta zamo mai tsayi; kuma saboda haka yake tashi ƙafafuwansa sun kumbura sun tsattsage".
Daga Abdullahi ɗan Mas'ud Allah ya ƙara masa yarda ya ce: "Na yi Sallah tare da (Annabi tsira da amincin Allah su ƙara tabbata a gare shi) sai yayi mana doguwar Sallah  har na nufaci aikata wani mummunan abu, sai aka ce masa me ka nufata? Sai ya ce na zauna

na bar shi (Annabi tsira da amincin Allah su ƙara tabbata gare shi) a tsaye!".
Ustaz Musa Shashin ya ce: " Babu shakka mafi alherin ambaton Allah shi ne Alƙur'ani, mafi alherin karantun Alƙur'ani kuwa shi ne wanda aka karanta a cikin Sallah, tare da tun-tun-tunin (bitar ma'anoninsa), haƙiƙa na ga wani daga cikin ma'abota ibada yana karanta dukkanin Alƙura'ani cikin kowanne dare na  cikin watan Ramadan. Zai ta da Sallarsa, sai ya karanta Fatiha, sannan ya karanta juzu'i ɗaya ko biyu, sannan sai yayi ruku'u da sujjada, sannan sai ya tashi ya karanta juzu'i ɗaya ko biyu, sannan ya sai yayi ruku'u da sujjada, sannan sai ya sake tashi ya karanta Fatiha da juzu'i ɗaya ko biyu, sai yayi ruku'u, haka yake yi wajen tsayuwarsa, wani lokacin kuma a zamansa yayin Sallar nafila. Na kasance ina mamakin irin wannan tsawaitawa sosai wacce (ba ni da tabbacin) hakan, har sai da na karanta wannan hadisi mai girma, kuma Annabi tsira da amincin Allah su ƙara tabbata a gare shi yayi Sallah a bayansa da akwai Huzaifatul yaman, ya karanta sama da juzu'i biyar (izu goma) a raka'a ɗaya (Baƙara, Nisa'i, Al'imra), wannan  abu ne mai girman gaske".
(Annabi tsira da amincin Allah su ƙara tabbata a gare shi), yayi umarni da sauƙaƙa karatu, kuma yayi gargaɗi kan tsawaita wa mutane a Sallar farilla".
Daga Abu Katada Allah ya ƙara masa yarda ya ce: "Manzon Allah tsira da amincin Allah su ƙara tabbata a gare shi, ya kasance yana karanta Fatiha da wata surar a ayoyin farko na Sallar Azahar da La'asar, da kuma Fatiha (ita kaɗai) a raka'o'in biyun ƙarshe, ya kasance wani lokacin yana jiyar da mu aya".
Wani mutum ya tambayi Abdullahi ɗan Umar Allah ya ƙara masa yarda cewa shin ana yin karatu a Sallar Azahar da La'asar? Sai ya ce: Shin Sallah za ta yiwu ne ba tare da karatu ba?".
Alƙadi Iyad ya ce: " Faɗin Abu Katada cewa, (Annabi tsira da amincin Allah su ƙara tabbata a gare shi) yana jiyar da mu aya, dalili ne a kan yin karatu a asirce ba sharaɗinta ba ne, sai ya jiyar da

wani abu daga cikinta, kamar yadda Annabi tsira da amincin Allah su ƙara tabbata a gare shi ya yi, ba tare da bayyanawa ba, domin ɗan bayyanawa kaɗan (ba tare da ɗaga murya ba), a wasu surorin a cikin raka'o'in da ake ɓoye karatu babu laifi (a kan hakan), sai dai abin da ya tabbata a karatunsa na raka'o'i biyun ƙarshe na Sallar Azahar da La'asar (shi ne) rabin waɗanda yayi a raka'o'in farko".
Imamun Nawawi ya ce: "Faɗinsa yana jiyar da mu aya, zai iya ɗaukar yana nufin, halaccin bayyana karatu (wani sashensa) a Sallar da ake ɓoyewa, kuma ɓoyewar ba sharaɗi ba ne na ingancin cikar Sallar, a'a shi hakan ma sunna ce, haka kuma bayyana ayar zai iya ɗaukar suɓul da bakan harshe saboda yadda zuciya ta yi nisa wajen tun-tun-tuni, Allah ne masani".
Ibnu Rajab Alhambali ya ce: " Abin da yake a bayyane (shi ne) Annabi yana jiyar da su aya, kuma zai iya yiwuwa yana hakan ne domin ya sanar da su cewa yana karatu a cikin Sallar Azahar da La'asar, domin wasu daga cikinsu (sahabai) sun taɓa shakka (game da shirun Annabi a Azahar da La'asar, na ganin cewa karatu yake yi, ko kuma shiru yake yi)".
Annabi tsira da amincin Allah su ƙara tabbata a gare shi ya kasance yana ɗaga hannayensa daidai kafaɗunsa a yayin kabbarar harama da lokacin da zai yi ruku'u.
Shamsuddin Alkarmani ya ce: "Al'umma sun haɗu a kan halaccin ɗaga hannu yayin kabbarar harama, kuma sun yi saɓani (wajen ɗaga hannu) bayan ta kabbarar harama, Imamu Shafi'I da Ahmad sun tafi a kan halaccin (ɗaga hannu) yayin ruku'u da yayin ɗagowa, Imam Abu Hanifa ya ce: Ba ya halatta a (ɗaga hannu) bayan na kabbarar harama, kuma shi ne mafi shaharar zantukan da aka rawaito daga Malik, sannan an rawaito daga wani sashe na mazhabar Hanafiyya a kan ɓacin Sallah (ga duk wanda ya ɗaga hannu bayan na kabbarar harama). Amma hikimar da ta sa ake ɗaga hannun kuwa; Imamush-shafi'i ya ce: Ana yin sa ne domin girmama Allah, da kuma bin Manzon Allah tsira da amincin Allah su ƙara tabbata a gare shi, wasu kuma suka ce ƙanƙantar da kai, da Sallamawa tare da miƙa

wuya, (kamar yadda) fursunan yaƙi idan aka ci galabarsa, sai ya miƙa hannu, alamar ya miƙa-wuyansa, (wasu kuma) suka ce: Alama ce ta nuna girman abin da za a shiga, (wasu kuma) suka ce: Alama ce da take nuna kore lamuran duniya, tare da tattaro hankalinsa da lamuransa domin fuskantar Sallarsa (a cikin nutsuwa da kushu'i), da kuma ganawa da Ubangijinsa, Allah shi ne masani".

Imamul Badawi ya ce: "Dukkanin malaman mazhaba sun haɗu a kan sunnanta ɗaga hannu yayin kabbarar harama, kuma sun yi saɓani game da yadda ake ɗaga shi, Imamu Malik da Ahmad sun tafi a kan sunna ne mutum ya ɗaga hannunsa kusa da kafaɗarsa, Abu Hanifa kuma ya ce daf da kunnuwansa".

Sheikh Usaimain yake faɗa game da hadisin da yake bayanin siffar Sallar Annabi tsira da amincin Allah su ƙara tabbata a gare shi: "Kuma sanin yadda siffar Sallar Manzon Allah tsira da amincin Allah su ƙara tabbata a gare shi wajibi ne, saboda kowanne aiki ba a karɓa sai da dalilai biyu: Tsarkake zuciya, da bin koyarwarsa, shi kuwa kwaikwayo, ba ya yiwuwa, sai mun san yadda Annabi tsira da amincin Allah su ƙara tabbata a gare shi yake bauta wa Allah, sannan mu bi shi".

Imamul Kaɗɗabi yake cewa game da hadisin da mahaifiyar muminai Aisha, Allah ya ƙara mata yarda ta rawaito wajen siffanta Sallar Manzon Allah; ta yadda yake fara Sallarsa da kabbara da kuma gama ta da Sallama: "Dalili ne a kan su waɗannan abubuwa guda biyu (kabbara da Sallama) rukuni ne, daga rukunan Sallah, wacce Sallah ba ta cika sai da su, saboda faɗinta yana fara Sallah da kabbara, kuma yana gama ta da Sallama, tana ba da labari game da abin da ya lazimta, kuma ya dawwama a kai, kuma (Manzon Allah tsira da amincin Allah su ƙara tabbata a gare shi ya ce) ya ce: *Ku yi Sallah kamar yadda kuka ga ina yi*".

Abulƙasim Arrafi'i ya ce:"Faɗin Annabi tsira da amincin Allah su ƙara tabbata a gare shi '*ku yi Sallah kamar yadda kuka ga ina yi*' kamar yana cewa ne 'kun zauna a wajena, kuma kun ga yadda nake

Sallah, kuma kun koye ta, to, idan kun koma garuruwanku, to ku yi Sallah kamar yadda kuka ga ina yi".

Abul Hassan Alau'ddin ya ce: "Ka sani koyin mamu (mai bin liman) wajen yin kabbara, da tsaiwa da zama, da ruku'u, da sujjada wajibi ne, kuma mai bin liman zai yi ne bayan liman ɗin yayi , sai ya yi kabbarar harama bayan liman ya gama tasa, idan ya fara yin kabbarar harama kuwa kafin liman, to, kabbarar ba ta yiwu ba; kuma zai yi ruku'u bayan limami yayi ruku'u kafin ya ɗago, (idan mai bin Sallah) ya haɗa ruku'unsa da na liman ko ya riga shi yin ruku'u; haƙiƙa ya saɓa, sai dai Sallarsa ba ta ɓaci ba, haka ma a sujjada, kuma zai yi Sallama bayan liman ya idar da Sallamarsa; idan kuma ya riga shi, to, Sallarsa ta ɓaci".

Almuzhiri ya ce: "Faɗin Annabi tsira da amincin Allah su ƙara tabbata a gare shi '*ku yi Sallah kamar yadda kuka ga ina yi*' yana nufin ku sanya ruku'unku da sujjadarku, da sauran rukunan Sallah, kamar yadda kuka ga ina yi".

Badruddin Al'aini ya ce: (Hadisin). '*Ku yi Sallah kamar yadda kuka ga ina yi*', (wajen) hakaito siffofin Sallarsa ta shiga ƙarƙashin wannan umarni (na kwaikwayon Sallarsa)".

Kaurani ya ce: "(Faɗin Annabi) '*ku yi Sallah kamar yadda kuka ga ina yi*' yana nufin a lokutanta, da sharuɗanta, da rukunanta".

Abu Yahaya Zakariyya Al'ansari ya ce: " Faɗin Annabi tsira da amincin Allah su ƙara tabbata a gare shi '*ku yi Sallah kamar yadda kuka ga ina yi*' a cikinsa da akwai umarnin bin Annabi tsira da amincin Allah su ƙara tabbata a gare shi, cikin zantukansa, da ayyukansa, da kuma Sallah da makamantanta. da koyi da shi cikin komai nasa". (sai dai idan abubuwan da suke keɓantattu ne a gare shi, shi kaɗai, kamar yin mata sama da huɗu da kuma zarcewa da azumi ba tare da shan ruwa ba).

Imamus Sun'ani ya ce: "Faɗin Annabi tsira da amincin Allah su ƙara tabbata a gare shi, '*ku yi Sallah kamar yadda kuka ga ina yi*' umarni ne ga dukkanin mai Sallah, kamar Sallarsa, tsira da amincin Allah a gare shi (yayin) jam'i ko shi kaɗai".

Sheikh Usaimin ya ce: "Manzon Allah tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi ya ce '*ku yi Sallah kamar yadda kuka ga ina yi*' wajibi ne (mutum) ya san yaya Manzon Allah tsira da amincin Allah su ƙara tabbata a gare shi yake Sallah, kuma ya aikata kamar yadda Manzon Allah yake yi, ta wannan ɓangare yana zama mafi girman nauyi, ta yadda wasu limaman suna yi wa mutane Sallah, (amma), ba sa nutsuwa a ruku'unsu, ko a ɗagowarsu daga shi, ko sujjadarsu ko yayin ɗagowa daga sujjadu biyu; wannan hatsari ne mai girma; musamman ma idan a masallacin da akwai (dattijai) masu shekaru, ko raunana".

Abdullahi bin Abdurrahaman bin Saleh (Albassam) ya ce: "Haƙiƙa Manzon Allah tsira da amincin Allah su ƙara tabbata a gare shi ya ce '*ku yi Sallah kamar yadda kuka ga ina yi*' ya wajaba a kan mu musan (yadda) yake Sallahrsa da kula da ita, duba da ayyukansa, mai tsira da aminci, bayani ne ga ayyukan da suke wajibi a cikin Sallah; domin ayyukansa, mai tsira da aminci, a cikin Sallah suna nuni da wajibi".

## 4.4 TASIRIN YIN IRIN SALLAR ANNABI (S.A.W)

Ba shakka akwai tasiri mai ƙarfi ga wanda yake yin irin Sallar da Ma'aiki tsira da amincin Allah su ƙara tabbata a gare shi yayi, wajen gyaruwarsa ta fuskar ƙarfin imani da lafiyar jiki, da nesantar dukkanin abin da Allah ba ya so; kamar yadda Allah ya faɗa a cikin Suratul Ankabut: "*Lallai Sallah tana yaye alfasha da dukkanin abin ƙi* (watau Sallah tana hana munanan ayyuka).

Daga cikin tasirin yin irin Sallar Manzon Allah tsira da amincin Allah su ƙara tabbata a gare shi da akwai nutsuwa, da kushu'i. Ga dukkanin wanda yai koyi da irin Sallarsa, to, shi ma zai samu nutsuwa da kwanciyar hankali a cikin Sallarsa; saboda yaƙini da yake da shi, na umarnin wanda ya ce a yi hakan.

Haka a cikin kwaikwayon Sallarsa da akwai nemawa kai tsari, ta yadda yake neman tsari daga abubuwan ƙyama, tun daga kan wuta da fitintinun rayuwa da fitinar Dujal, da dukkanin wasu nu'ika na abubuwan ƙyama a lokacin da mutum yake da rai, ko bayan haka.

Sannan a cikin koyi da Sallarsa akwai ambaton Allah, da yadda ake yabon Allah da irin yabon da ake masa a kowanne rukuni na Sallah, shi kuwa mai ambaton Allah a bisa koyi da yadda Manzon Allah tsira da amincin Allah su ƙara tabbata a gare shi yake yi. Alama ce ta kyakkyawar rayuwar da mutum yake yi, kuma hakan nutsuwa ce da kwanciyar hankali a gare shi, sannan bawa zai zamo abin ambato a wajen Allah da waɗanda suke wajensa. Allah Maɗaukakin Sarki yake faɗa:

(ΣYHIJNŭ IIY Ʃɑɿ ẙYHJNhẙY ɓJNHJNĸừ ƩţYHJNĸŸƕʊ)

*"Ku tunani (ambaceni) zan tuna ku, ku gode min, kar ku butulce min".*

**(الَّذِينَ آمَنُوا وَتَطْمَئِنُّ قُلُوبُهُمْ بِذِكْرِ اللهِّ أَلا بِذِكْرِ اللهِّ تَطْمَئِنُّ الْقُلُوبُ)**

*"Zukatan waɗanda suka yi imani sukan nutsu da ambaton Allah. To, (lallai), da ambaton Allah zukata suke nutsuwa".*

Dukkanin waɗannan ayoyi suna nuni game da ambaton Allah, wanda a cikin koyi da Sallarsa da akwai ambaton Allah da samun nutsuwa. A wani hadisin kuma Manzon Allah tsira da amincin Allah ssu ƙara tabbata a gare shi yake cewa: "*Misalin wanda yake ambaton Ubangijinsa, da wanda ba ya ambatonsa, kamar misalin rayayye da matacce ne*".

Daga cikin tasirin da musulmi zai samu wajen yin irin Sallar Manzon Allah tsira da aminci Allah su ƙara tabbata a gare shi, da akwai ladan koyi da Annabinsa.

## 4.5 Hatsarin Saɓa Wa Sallar Annabi

Saɓawa Manzon Allah tsira da amincin Allah su ƙara tabbata a gare shi babban hatsari ne da mutum yake tattare da shi a cikin rayuwarsa, daga cikin waɗannan munanan sakamako da mutum zai fuskanta sanadiyyar saɓa wa Annabi tsira da amincin Allah su ƙara tabbata a gare shi su ne:

- Halaka a duniya da lahira, wajen faɗawa cikin musifu da fitintinu, Allah Maɗaukaki yake cewa:

(فَلْيَحْذَرِ الَّذِينَ يُخَالِفُونَ عَنْ أَمْرِهِ أَنْ تُصِيبَهُمْ فِتْنَةٌ أَوْ يُصِيبَهُمْ عَذَابٌ أَلِيمٌ )
"To waɗanda suke saɓa wa  umarninsa su ji tsoron, wata fitina ta same su, ko wata azaba mai raɗaɗi"."
Wannan aya tana nuna hatsarin da mutum zai shiga, idan ya saɓa wa Annabi tsira da amincin allah su ƙara tabbata a gare shi, ba wai kawai a sallarsa ba, har dukkan al'amuransa da tsarin rayuwarsa wajen kiran mutane zuwa ga Allah da yi masu gargaɗi akan hanyar da ba ta ɓullewa da kyawawan tsarin rayuwarsa a cikin iyalinsa da kuma almajiransa (sahabbansa). Sa'an nan ya faɗa cikin halaka kamar yadda yake cewa: "*Lallai abin da ya halakar da waɗanda suke kafin ku (shi ne) yawan tambayoyinsu (marasa amfani) da saɓa wa Annabawansu*".

- Daga cikin hatsarin saɓawa irin Sallar Annabi tsira da amincin Allah su ƙara tabbata a gare shi, shi ne rashin karɓar Sallar; saboda ba ta dace da irin wacce shari'a ta umarta ba, kuma Manzon Allah tsira da amincin Allah su ƙara tabbata a gare shi ya ce: "*Duk wanda yayi wani aiki wanda babu umarninmu a cikinsa, to shi abin mayarwa ne*".
- Daga cikin hatsarin saɓa wa irin sallar ma'aikin Allah,  watsi da umarnin sa; domin ya ce: *Ku yi Sallah kamar yadda kuka ga ina yi*". Kuma ya ce: "*Duk abin da nazo muku da shi, ku riƙe shi, abin da na hane ku kuma, ku nesance shi*".
- Dukkanin wanda ya saɓa masa, wajen ƙin bin umarninsa ko irin aikinsa zai kasance a cikin ɓata da ruɗani, har ya zamanto dukkanin al'amura sun hargitse masa.
- Daga cikin hatsarin da bawa zai shiga, sanadiyyar saɓawarsa ga irin Sallar Annabi tsira da amincin Allah su ƙara tabbata a gare shi, zai zamo ya bi son zuciya da zalunci; saboda ya fifita aikinsa da ra'ayinsa ko jahilcinsa sama da na Annabin Rahama, wanda shi ma yin haka  hatsari ne mai girma, domin shi mumini ba shi da zaɓi ko ra'ayi matuƙar abu ya zo daga Allah da Manzonsa, wanda aikata saɓanin hakan kuwa shi ne yake buɗe wa mutum dukkanin ƙofofin halaka da son zuciya, da

ruɗin duniya, Allah Maɗaukaki da buwaya ya faɗa a cikin littafinsa mai girma:

**(وَما كانَ لِمُؤْمِنٍ وَلا مُؤْمِنَةٍ إِذا قضَى اللهُّ وَرَسُولُهُ أَمْراً أَنْ يَكُونَ لَهُمُ الْخِيَرَةُ مِنْ أَمْرِهِمْ وَمَنْ يَعْصِ اللهَّ وَرَسُولَهُ فَقَدْ ضَلَّ ضَلالاً مُبِيناً).**

"Ba ya halatta ga mumini ko mumina, a lokacin da Allah da Manzonsa suka zartar da wani umarni (hukunci), ya zamanto suna da zaɓi (ra'ayin su ko tunanin su ko kuma son zuciyar su) a cikin al'amarinsu, kuma wanda ya saɓa wa Allah da Manzonsa, to, ya ɓata, ɓata mabayyani".

## KAMMALAWA

Haƙiƙa ni'imomin Allah a kan bayinsa ba za su ƙidayu ba, ba ƙaramar ni'ima ba ce Allah ya yarje wa bawa ya tsaya ya yi bincike na ilimi, don ya fito da haƙiƙanin ibada mafi girma ita ce Sallah, dukkanin wani alherin duniya da lahira ya tattaru wajen yin Sallah irin ta Ma'aiki tsira da amincin Allah su ƙara tabbata gare shi da kuma zaƙulo kurakurai manya da ƙanana da zana su da bayyana hatsarin aikata su da jan hankali akan nisantar su.

A ƙarshe ina roƙon Allah Maɗaukakin Sarki da ya sanya karɓuwa ga ɗan wannan aikin a gurinsa da kuma duniyar Musulunci, Allah ya sanya mu daga cikin masu yin Sallah irin ta Ma'aiki tsira da amincin Allah su ƙara tabbata a gare shi, shi mai cikakken iko ne a kan komai.

**وصلى الله وسلم وبارك على حبيبنا وشفيعنا ومولانا، محمد وآله وصَحْبِهِ وَمَنْ تَبِعَهُمْ بإحسَانٍ إلى يَوْمِ الدِّين، وآخر دعونا عن الحمد للهَّ رب العالمين.**

JERIN LITATTAFAN DA AKA DUBA


- Alƙuranil Karim
- Tarjamar Alƙur'ani: Sheikh Abubakar Mahmud Gumi
- Azzakhira: Imamul ƙarafi
- Al'istizkar Sharh Muwaɗɗa Malik: Ibn Abdul-barr
- Almafatihu Fi Sharshil Masabih
- Al'udda Fi Sharshihil Umda Fi Ahadisil Ahkam: Aliyu bin Ibrahim bin Dawud bin Salman bin Sulaiman
- Alkausarul Jari Ila Riyad Ahadis Bukhari: Ahmad bin Isma'il bin Usman bin Muhammad (Alkaurani)
- Al'ausaɗ Fis Sunani Wal Ijma Wal Iktilaf
- Al'ibda'u
- Al'ifsahu An Ma'anissiha: (Yahya bin Hubaira)
- Alfatahur Rabbani bitartibi Musnad Ahmad
- Alminhaj, Sharhu Sahih Muslim: Abu Zakariyya (Imamun Nawawi)
- Alkawakibud-durari, Fi Sharshi Sahihil Bukhari: Muhammad bin Yusuf bin Ali bin Sa'id (Shamsuddin Alkarmani)
- Almuktafa:
- Almadkal
- Alfiƙihul Muyassar: Nukbatun Minal Ulama'I
- Alwajiz fi Fiƙhis Sunna wal Kitabil Aziz: Dokta Abdul'azim Badawi
- Fatahu Zil Jalal Wal'ikram, Bi sharsh Bulugul Maram: Muhammad bin Saleh Al'usaimin
- Fatahul Bari, Libni Rajab: Zainuddin Abdurrahman bin Ahmad bin Rajab bin Alhasan (Ibnu Rajab Alhanbali).
- Fatahul Allam Bi Sharhil I'Ilam Fi Bi Ahadisil Ahkam: Shaikul Islam Abu Yahya Zakariyyal Ansari Asshafi'i
- Fatahul Mun'im Sharh Sahihu Muslim: Ustaz Doktor Musa Shashin,
- Fiƙihul Muyassar: Sa'ad Yusuf Abdul'aziz
- Fiƙihus-sunna: Sayyid Sabiƙ

- Sahihul Bukhari: Abu Abdullahi Muhammad bin Isma'il Albukhari
- Sahihu Muslim: Abul Hasan Muslim bin Hajjaj
- Sunan Abi Dawud: Abu Dawud Sulaiman bin (Ash'as)
- Sunanun Kubura: Abu Abdurrahman Ahmad bin Shu'aib Annasa'i
- Sunanus-sugra: Abu Abdurrahman Ahmad bin Shu'aib Annasa'i
- Sunan Bin Majah: Abu Abdullahi Muhammad bin Yazid bin Majah
- Sahihu Ibnu Kuzaima: Abubakar Muhammad bin Ishaƙ (Ibnu Kuzaima)
- Sharhus-sagir Sharhu Riyad Salihin: Muhammad bin Saleh bin Muhammad Al'usaimin
- Sharhu Musanad Asshafi'i: Abdulkarim bin Muhammad bin Abdulkarim (Arrafi'I Alƙazwaini)
- Sharhul Mumti Muhammad bin Sale Al'usaimin
- Sifatus Salatin Nabiy: Muhammad Nasuruddin Albani
- Taisirul Allam Sharh Umdatil Ahkam: Abu Abdurrahman Abdullahi bin Abdurrahman bin Saleh bin Hamd bin Muhammad,
- Talkisu Sifati Salatin Nabiyi: Muhammad Nasuruddin Albani
- Muwaɗɗa Malik bin Anas
- Minhajul Muslim: Abubakar Jabir Aljaza'iri, Maktabatul Ulum wal hikam
- Nurul Basa'ir, Wal'albab
- Al'ijma'i
- Ihyaus-sunna: Usman bin Fodiyo
- Ikmalul-mu'ulim: Iyad bin Musa bin Iyad (Alƙadi Iyad)
- Jamiut-tirmizi: Abu Isa Attirmizi
- Kifayatul Akyar: Abubakar bin Muhammad bin Abdulmumin bin Hariz
- Majmu'u Fatawa Wa Rasa'il

- Akɗa'ul Musallin Alal Mazhabil Maliki: Ahmad Musɗafa Kasim Aɗɗahɗawi, Daril Fadila
- Akɗa'ul Musallin: Muhammad Siddiƙ Almunshawi, Darul-fadila
- Musnad Imam Ahmad bin Hanbal
- Matnul Akhdari: Asheikul Allama, Abdurrahman Al'akdari
- Mukhtasar Khalil: Imam Khalil bin Ishaƙ Aljundi
- Mu'alimus-sunan: Abu Sulaiman Hamd bin Muhammad bin Ibrahim bin Kaɗɗab (Alkaɗɗabi)
- Mawahibul Jalil,
- Zadul Ma'ad: Ibnul Kayyum Azzauji
- Wabalul Gamama Fi Sharhi Umdatil Fiƙhi
- Umdatul Kari Sharsh Sahih Albukhari: Badruddin Al'ain

Wasu Litattafan Mawallafin dake kan Hanya sun Haɗar da:

1. Haƙiƙanin Janaza a Musulunchi da Kurakuranta
2. Rayuwar Aure a Musulunchi Da Kurakuransa
3. Fassarar Sharhin Ahlari na Dr. Aminuddeen
4. Tsarin Da'awa a Musulunchi da Kurakuranta
5. Hanyoyin Cin Nasara a Rayuwa
6. Usulul Iman wa Thamaratuhu lilma'ahidi wal Kulliyat
أصول الايمان وثمراته للمعاهد والكليات
7. Fassarar Littafin Ta'alimul Muta'allim na Burhanuddeen Ibrahim

Ga mai buƙatar ɗaukar nauyin buga ɗaya daga cikinsu (ko duka) sai ya tuntuɓi Cibiyar Fassara ta Ar-Rahyan ta waɗannan kafofin:

Adireshi:
Dr. Abubakar Fari Residence,
Juma Road, Mariri, Maiduguri Road, Kano. Nigeria
GSM: 08036223067
Whatsapp: 07049325138
Email: abuamatullahi83@gmail.com